**COURSE GUIDE**

# HAU 204
# INTRODUCTION TO THE ORAL LITERATURE OF HAUSA

**Course Team** Dr. Aliyu Isa Sulaiman(Marubuci)-Kaduna State Uniƃersity Kaduna
Professor Ibrahim Malumfashi (Wanda ya tace Rubutu)-Kaduna State Uniƃersity Kaduna

NATIONAL OPEN UNIƁERSITY OF NIGERIA

© 2023 by NOUN Press
National Open Uniϐersity of Nigeria
Headƙuarters
Uniϐersity Ɓillage
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Edƥressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Ɓictoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserϐed. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Published by:
National Open Uniϐersity of Nigeria

Printed 2022

ISBN:978-978-058-456-5

## CONTENTS

Gabatarwa (Introduction)…………………………………………… iv
Koyo Tsantsa (Working Through the Course)……………………… iv
Kashe-kashen Darasi (Study Units) ……………………………….. iv
Manazarta da Abubuwan Ƙara Nazari:…………………………….. iv
Auna Fahimta (Assignment)………………………………………. v
Jinga (Tutor Marked Assignment)……………………………… vi
Jarrabawa (Final Eɗamination and Grading)…………………….. vii

## Gabatarwa (Introduction)

Wannan darasi na HAU204, kwas ne da ke bayyana yadda adabin baka na Hausa yake. Bayanan dake cikin wannan manhaja suna gabatar da wannan darasi ne tun daga ma'ana ita kanta kalmar adabin baka da manufar adabin baka. Haka nan kuma an yi bayanin rabe-raben adabin baka waɗanda suka haɗa da waƙar baka da zube nab aka da kuma wasannin kwaikwayo na baka. Wannan manhanja tana bayani kan abin da kwas ya ƙunsa da kuma abubuwan da kwas yake bukata da kuma bayanan da ɗalibai za su yi amfani da su domin fahimtar kwas sosai da sosai. Manhajar na bayanin irin abubuwan da suka kamata ga ɗalibi ya kiyaye a yayin da yake nazarta kowane kashi. Haka nan kuma, manhajar ta kawo tambayoyi waɗanda ake bukatar mai nazari ya amsa, don yin haka zai taimaka wajen fahimtar abin da kwas din yake koyarwa. Yana da kyau idan an sami matsololi ko rashin fahimtar wani kashi ko darasi a garzaya faɗin haka a yayin tattaunawa da malaman da ke kula ko koyar da wannan darasin. Ya zama wajibi a rinƙa tuntubar malami ko malamai kan wasu abubuwan da suka shigewa ɗalibai duhu a yayin da ake tattaunawa tsakanin malamai da ɗalibai (tutorial class). Yin haka zai taimaka ainun wurin samun nasarar isar da sako ga ɗalibi.

## Manufar Wannan Kwas (Course Aim)

An karkasa wannan kwas na HAU204 zuwa kashi kashi, a kowane kashi, akwai muhimman abubuwa da ake fatar ɗalibai su sani game da kowane kashin da aka gabatar, wato manufar da ake ƙoƙarin a cimmawa yayin da aka kammala karatun wannan kashin. Don haka, a karanta manufar da kyau a kuma fahimce ta sosai da sosai. Da zarar an san manufar da wannan kashi ko darasi take fatar ta cimma wa, to ɗalibai za su iya gwada ƙimar ganewarsu ko rashin gane darasin da suka karanta.
Wannan darasi na (HAU204) na da muhimman manufofin da yake ƙoƙarin isar wa ga mai karatu waɗanda suka haɗa da:

- Ma'ana da rabe raben adabin baka
- Siffofin adabin baka
- Matsalolin tattara adabin baka
- Hikimomin zantukan baka na Hausa

## Koyo Tsantsa (Working Through the Course)

Idan an tsunduma cikin wannan kwas, ana buƙatar a nazarci kowane kashi a tsanake tare da bibbiyar manazaratar da aka gabatar domin ƙarin haske da samun ƙarin bayanai. Sanannen abu ne cewa Hukumar NOUN ta tanadar wa ɗalibai muhimman abubuwa da ɗakin karatu duk ta yanar gizo waɗanda za su taimakawa ɗalibi karatu daga gida, ba don komai ba sai don inganta karatunsu da kaifafa fahimtar abin da aka sa wa gaba. A

ƙarshen kowane kasha na wannan kwas, akwai tambayoyi, su waɗannan tambayoyin an yi su ne domin su auna fahimtar mai karatu dangane da abin da ya karanta. Haka nan kuma akwai JINGA (Tutor Marked Assignment) waɗanda aka tsara domin ɗalibai. Ana bukatar idan an amsa waɗannan tambayoyi, to a miƙa amsoshin ga malaman da ke kula da darasin domin a duba a kuma bayar da sakamakon da ya cancanta. Su waɗannan ayyuka na "Jinga" da aka ba ɗalibai suna taimakawa wajer harhaɗa sakamakon jarabawar ƙarshen zangon karatu domin fitar da sakamakon kowane kwas da ɗalibai suka yi. Rukunai guda huɗu wannan kwas na HAU204 yake da su, a kowane rukuni akwai kasha kasha huɗu huɗu, saboda haka ana sa ran ɗalibai su kammala wannan kwas cikin satuttuka goma sha shida kwatankwacin yawan kashin da ake da su. Kowane rukuni yana da alaƙa da mai bi masa, haka nan kowane kashi yana da dangantaka da mai biye da shi. Saboda haka, kada ɗalibai su tsallake wani kashi zuwa wani kashi, yin haka kan gungurta fahimta da rashin gane abin da kwas yake koyarwa.

Tsara lokacin karatu da ɗalibai za su yi dai-dai da yawan kashe-kashen da ke kowane kwas ita ce muhimmiyar shawarar da ake basu, saboda a sami nasarar kammala kashi kashin da ke cikin kwas cikin lokaci. Idan ɗalibi ya kammala karatu cikin lokaci, yana da damar sake bitar abubuwan da aka yi a baya kafin jarabawar ƙarshen zangon karatu.

Muhimman abubuwan da suka shafi wannan kwas sun haɗa da:

a. Rarraba rukunin zuwa kashi – kashi (study units)
b. Manazarta da abubuwan kara nazari (reference)
c. Tambayoyi na auna fahimta (jinga). Assignment file
d. Tarin gabatar da Darasi (presentation schedule)

**Kashe-kashen Darasi (Study Units)**

Bayanai sun gabata waɗanda ke nuna cewa wannan kwas HAU204 na ƙunshe da kashi-kashi har guda goma sha shida. Ana bukatar a kammala kowane kashi cikin sati guda ne wanda ya haɗa har da amsa tambayoyi da ke ƙarshen kowane kashi da kuma amsa tambayoyin jinga idan akwai shi a ƙarshen darasin. Wannnan kashe-kashen su ne;-

**Rukuni Na 1 Ma'ana Da Rabe-Raben Adabin Baka**

Kashi Na 1 Ma'anar Da Manufar Adabin Baka
Kashi Na 2 Rabe-raben Adabin Baka: Waƙar Baka
Kashi Na 3 Zube na Baka
Kashi Na 4 Wasannin Kwaikwayo Na Baka

**Rukuni Na 2 Siffofin Adabin Baka**

Kashi Na 1 Tsari
Kashi Na 2 Harshe
Kashi Na 3 Wanzarwa
Kashi Na 4 Saurare

**Rukuni Na 3 Matsaloli Tattara Adabin Baka**

Kashi Na 1 Matsalar Rashin Rubutu/Adana
Kashi Na 2 Matsalar Shekaru
Kashi Na 3 Al’ada
Kashi Na 4 Ragi ko Ƙari

**Rukuni Na 4 Hikimomin Zantukan Baka Na Hausa**

Kashi Na 1 Karin Magana
Kashi Na 2 Salon Magana
Kashi Na 3 Take Da Kirari
Kashi Na 4 Zaurance

**Manazarta da Abubuwan Ƙara Nazari**:

A ƙarshen kowane kashi akwai manazarta wanda zai taimakawa ɗalibai ƙara nazari da zurfafa bincike. Wasu daga ciki litattafai ne waɗanda ba masu wuyar samu ba ne a ɗakunan sayar da littafai musamman waɗanda ke sayar da na Hausa. Akwai littattafan adabin baka na Finnegan, (1970) da na Ɗangambo, (2008) da Babajo, (2011) da Okoh, (2008) waɗanda ya kamata ɗalibai su nemo su don su ƙara karatu. Wasu kuma kundaye ne na kammala karatu digiri na ɗaya da na biyu hard a digirin digirgir, wasu kuma muƙalu ne ko dai a Mujallu ko waɗanda aka gabatar a tarurukan ƙara wa juna sani. Wasu daga ciki za a iya samunsa ta kafar sadarwa ta yanar gizo, ko kuma da taimakon ɗakunan karatu na Jami’o’i, musamman jamai’ar da take kula da “karatu daga gida” idan littattafan sun yi ƙaranci, ko kuma wuyar samu, to yana da kyau a yi amfani da bayanan da wannan manhajar kwas ɗin ya samar

**Auna Fahimta (Assignment)**

Gwaji da ake wa ɗalibai domin gane fahimtar su a wannan kwas suna kasancewa ta hanyoyi guda biyu ne. Hanya ta farko ita ce, ta ayyukan da ake ba ɗalibai su yi domin a gyara. Hanya ta biyu ita ce, wadda ake jarraba ɗalibai a ƙarshen zangon karatu (eɗamination). Da yake yanzu komi na koyarwa sun koma ta na’urar mai ƙwaƙwalwa ce, haka ma jingar da ake ba ɗalibai. Ana basu ne kuma suna amsawa da turowa nan take da zarar

su gama amsa tambayoyin da aka yi masu. Daga nan ba tare da jimawa ba za su sami sakamakon jarrabawar da suka yi. Yana da kyau a kiyaye lokaci wajen amsa kowace tambaya domin yin haka kan taimaka wajen amsa tambayoyi duka cikin lokaci. Ana sa ran ɗalibai su amsa tambayoyin JINGA aƙalla guda uku waɗanda daga cikin ukun nan ne za a zaɓi ƙwarara guda biyu waɗanda ɗalibi ya fi samun maki don su kasance kashi talatin cikin ɗari na jararrawa (30%), sauran kashi saba'in (70%) ana samunsu ne a jarrabawar ƙarshen zangon karatu (semester eɗamination). Ita wannan jarrabawar zangon ƙarshen karatu, ana yin ta ne ta hayar yanar gizo, saboda haka yana da kyau ɗalibai su kasance sun gwane da naƙaltar na'u'rorin kwamfuta saboda a sami cin jarrabawa yadda ya kamata.

**JINGA (Tutor Marked Assignment)**

Ɗalibai za su iya gwada fahimtarsu game da wannan kwas ta ƙoƙarin amsa tambayoyin da ke ƙarshen kowane kashi. Dole kowane ɗalibi ya san manufar kowane kashi na darussan da suka gabata. Idan ya san haka ne zai iya gwada fahimtarsa ta hanyar amsa tambayoyin da ke biye a kowane kashi. Duk da cewa jarrabawar da ake ba ɗalibai ta yanar gizo suke, duk da haka ɗalibai za su iya gwada fahimtarsu ta ƙoƙarin amsa tambayoyin da ke ƙarshen kowane kashi.

**Jarrabawa (Final Eɗamination and Grading)**

Ya kamata ɗalibi ya sani cewa jarrabawar ƙarshen zangon karatu na ɗaukar kashi saba'in (70%) cikin ɗari na sakamakon da ya kamata ɗalibi ya samu. Akan ciro tambayoyin da ɗalibai za su amsa daga cikin ire-iren tambayoyin da ake yi a ƙarƙashin auna fahimta ta ƙarshen kowane kashi. Don haka yana da kyau ɗalibai su yi ƙoƙarin amsa waɗannan tambayoyin da aka yi masu a ƙarshen kowane kashi da aka gabatar, ana son a yi amfani da kyakykyawar Hausa da misalai masu kama hankali.

**MAIN COURSE**

## CONTENTS

**Rukuni Na 1 Ma’ana Da Rabe-Raben Adabin Baka... 1**

Kashi Na 1 Ma’anar Da Manufar Adabin Baka……………… 1
Kashi Na 2 Rabe-raben Adabin Baka: Waƙar Baka…………. 9
Kashi Na 3 Zube na Baka…………………………………… 24
Kashi Na 4 Wasannin Kwaikwayo Na Baka………………… 30

**Rukuni Na 2 Siffofin Adabin Baka…………………… 38**

Kashi Na 1 Tsari……………………………………………… 38
Kashi Na 2 Harshe…………………………………………… 45
Kashi Na 3 Wanzarwa……………………………………….. 49
Kashi Na 4 Saurare………………………………………….. 52

**Rukuni Na 3 Matsaloli Tattara Adabin Baka………. 57**

Kashi Na 1 Matsalar Rashin Rubutu/Adana………………… 57
Kashi Na 2 Matsalar Shekaru……………………………... 62
Kashi Na 3 Al’ada…………………………………………… 66
Kashi Na 4 Ragi ko Ƙari…………………………………….. 71

**Rukuni Na 4 Hikimomin Zantukan Baka Na Hausa… 76**

Kashi Na 1 Karin Magana………………………………….. 76
Kashi Na 2 Salon Magana………………………………….. 81
Kashi Na 3 Take Da Kirari………………………………… 85
Kashi Na 4 Zaurance………………………………………. 89

# RUKUNI NA 1 MA'ANA DA RABE-RABEN ADABIN BAKA

Kashi Na 1 Ma'anar Da Manufar Adabin Baka
Kashi Na 2 Rabe-raben Adabin Baka: Waƙar Baka
Kashi Na 3 Zube na Baka
Kashi Na 4 Wasannin Kwaikwayo Na Baka

## Kashi Na 1 Ma'ana Da Manufar Adabin Baka

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma'anar Adabin Baka
1.3.1 Ko Mutanen Afirka na da Adabi?
1.3.2 Ra'ayoyin Turawa
1.3.3 Ra'ayoyin 'Yan Afirka
1.4 Manufar Adabin Baka
1.4.1 Gina Tunani
1.4.2 Koyar Da Tsarin RayuwaAuna Fahimta
1.5 Taƙaitawa
1.5.2 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa (Introduction)

Adabin baka wanda wasu ke kira da adabin gargajiya ko adabin 'ka', adabi ne wanda da can aka fi danganta shi da mutanen da ilimin rubutu bai kai gare su ba a yayin da suka ƙirƙiri wannan adabi. Wani lokaci ana danganta wannan adabi da lokutan kaka da kakannin da suka shuɗe, ire-iren adabin su shi ake wa laƙabi da adabin gargajiya, wato adabin da suka samu kafin a fara cuɗanya da wata baƙuwar al`ada ko mutane. Kashin ya duba ma`anar adabin baka da rabe-rabensa daga bakin masana, da kuma yadda adabin baka ya yaɗu a cikin al`ummar Hausawa da yadda matsayin nazarin adabin yake a halin da muke ciki.

Dalilai da dama sun tabbatar da nazarin adabin baka abu ne mai mutuƙar muhimmanci ga kowace al`umma, sanannen abu ne cewa akwai dangantaka tsakanin adabin baka da al`ummar da take da wannan adabin. Saboda haka wajen nazartar al`umma yana da kyau a nazarci adabinta wajen gane yadda take rayuwa da falsafarta game da rayuwa. Muhimman manufofin adabin baka su ne, faɗakarwa da kuma ilmantarwa da kuma nishaɗantarwa, rai dangin goro ne ban iska yake

buƙata. Don haka, nishaɗi ga rayuwar ɗan Adam abu ne da masana ilimin walwalar ɗan Adam suka tabbatar da muhimmancinsa.

Rayuwa ba za ta ingfanta ba, ba tare da an sami lokaci na hutu tare da walwala domin ƙwaƙwalwa ta sanyaya don fuskantar al`amurorin rayuwa nan gaba ba. Ashe idan an sami nishaɗantar wa wanda zai taimakawa ƙwaƙwalwa ta sami sauƙin gudanar da ayyukanta na yau da kullum ko da kuwa bincike-binciken kimiyya da fasaha ne ko ƙere-ƙere an sami nasara. Adabin baka a matsayinsa na wata kafa mai nishaɗantar da al`umma na taka muhimmiyar rawa wajen cusa nishaɗi ga zukatan jama`a. Baya ga wannan, nazartar adabin baka ya zama wajibi domin kuwa yana ilmantar da al`umma domin su gane tafarkin rayuwa da yadda ya kamata su fuskanci kowane ƙalu-bale a rayuwarsu.

## 1.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Ana fatar yayin da aka kammala wannan darasi, ɗalibai su iya fahimtar ma`anar adabin baka da manufarsa da siffofin da suke bayyana adabin baka da kuma dalilan da suka sa Turawa ke ganin rubutaccen adabi ba shi da matsuguni a al`ummar Afirka. Ba a nan darasin ya tsaya ba, ana sa ran mai karatu ya fahinci dalilan da suka sa ake nazarin adabin baka da kuma fa`idar da ke tattare da adabin baka don ci gaban al`umma.
Ƙunshiyar Darasi

## 1.3 Ma'anar Adabin Baka

Adabin baka na nufin hikima da fasahar al`umma waɗanda aka ƙirƙirƙa a 'ka', aka adana a 'ka', kuma ake wanzarwa ta baka. Wannan na nufin hikimar da aka ƙirƙire ta tun samuwarta ba tare da an rubuta ta ba. Ana samun adabin baka duk da ci gaban da aka samu na ilimin rubutu da kayayyakin ƙere-ƙere irin na zamani kamar su Jaridu ko rediyo ko talbijin da na`u`rori masu ƙwaƙwalwa. Idan an fahinci ma`anar da aka gabatar, ashe ko a wannan zamani da muke ciki za a iya samar da adabin baka. Wato hikimar da aka ƙirƙira da 'ka' aka wanzar ta baka sa`annan kuma wurin adanarta ƙwaƙwalwa ce ba tare da an yi amfani da wata kafa ta rubutu ko na`ura ba. Saboda haka adabin baka na nufin hikimomin da suka shafi waƙoƙin baka da labarai da tatsuniya da zantukan hikima irin su Karin magana da sauransu. A kan ƙara bayyana ma`anar adabi da cewa hikima da fasaha ce masu bayyana hoton rayuwar wata al'umma. Idan ana maganar adabin baka na Hausa, ana nufi hikimomi da fasahar Hausawa waɗanda ke bayyana hoton rayuwarsu ta fannoni da suka haɗa da zamantakewa, da tsarin shugabanci da tattalin arziƙi da ɗabi`u da falsafarsu game da rayuwa.

### 1.3.1 Ko Mutanen Afirka na da Adabi?

Idan aka yi amfani da kalmar Ingilishi ta 'Literature' wadda ita ce aka fassara ta da adabi, sai mu ce da can mai nisa, mutanen Afirka ba su da wani nau`in rubutuwaɗanda aka wallafa ko adana ire-iren hikimominsu a fasahohinsu na rayuwa.

Saboda haka, ba rashin iya karatu ko rubutu shi ke tabbatar da jahili ba, ba haka abin yake ba. Ilimi na samuwa ne a ƙwaƙwalwa kuma ta nan ne ake sarrafa shi a yi duk abubuwan da ake buƙata, Idan iya karatu da rubutu yana samuwa ne a ƙwaƙwalwa kafin a bayyana waɗannan hikimomin a rubuce, ashe waɗanda ke da hikimomi da fasahohi na rayuwa waɗanda suka keɓanta garesu su kaɗai, to ko shakka babu suna da adabi. Bambancin su kawai ba a wanzar da waɗannan hikimomin a rubuce ba ne. Da wannan za mu iya cewa in dai har sai an yi tunani da ƙwaƙwalwa kana a ƙirƙiri hikimar da za a rubutata (literature), za a iya bugun ƙirji da cewa mutanen Afirka suna da adabi.

### 1.3.2 Ra'ayoyin Turawa

Bayani ya gabata a sama na irin tunanin da wasu turawa suke da shi game da samuwar adabi a al`ummar Afirka ba ma Bahaushe kaɗai ba. Da yawa daga masu irin wannan ra`ayi, sun kasance turawan da suka ziyarci ƙasashen Afirka ko dai da niyyar yawon buɗe ido, ko niyyar watsa addinin Almasihu ko kuma da niyyar kasuwanci ko mulkin mallaka.

Da yawa daga cikin waɗannan ra`ayoyi an gabatar da su don kawai su kare muradin Tarawa ko don su ɓoye irin ɓarna da ta`asar da Turawa suka yi wa nayiyar Afirka. Wasu daga cikin turawan ma na ganin al`ummar baƙar fata baki ɗaya ba su da wata gudunmuwar da za suka bayar don ci gaban al`umma, haka nan ma ba wani iƙrari da za a iya yi na irin gudummuwar da baƙar fata ta bayar don ci gaban a al`adu a duniya, Nkoh, (2008). A ƙarni na sha-tara da ya wuce, an sami wani majami`in kirista Reɓerend J.L. Dohne (1857) wanda ya yanke ɗanyen hukunci game da rashin samun waƙa a adabin baka na al`ummar Zulu na ƙasar Afirka ta kudu, Anyidoho, (1985). Burton, (1956) da Stanley, (1906) a cikin Nkoh, (2008) da ma wasu da yawa waɗanda ba a ambata ba suna da irin wannan tunanin.

### 1.3.3 Ra'ayoyin 'Yan Afirka

Abu ne sananne cewa dole a samu raddi daga al`ummar baƙar fata waɗanda ba a ɗauke su a bakin komai ba wajen ilimi da hikima da fasaha da ma kyakykawar tsarin gunanar da rayuwa. Yunƙurin tabbatar da rashin sahihancin ƙirarin da turawa suke yi na rashin samun adabi ya

fito daga rubutun wani mutumi Igbo wanda ya kasance bawa a ƙasar turawa. Wasu abubuwa muhimmai sun bayyana a tarihin rayuwarsa da ya rubuta a 1798, daga cikin rubutun, an nuna ana samun waƙe-waƙe da kaɗe-kaɗe da shagulgula a duk lokacin da wani muhimmin al`amarin ya faru na baƙar fata. Misali idan aka dawo daga filin daga ko yaƙi ko hari, akan yi murna da kaɗe-kaɗe da waƙe-waƙe don girmama juruman da suka yi bajinta a fagen fama. Wannan ya nuna cewa samar da waƙe-waƙen da aka yi, sun nuna hikimomi da fasahar al`ummar da ta samar da su. Don haka kuskure ne a ce Afirka ba su da adabi.

## 1.4 Manufar Adabin Baka

Da yawa daga cikin mutane suna da ra`ayin cewa adabin baka ba shi da wani matsuguni wajen taimakawa da ci gaban al`umma ta fuskar kimiyya da ƙere-ƙere, musamman a wannan lokaci da muke ciki na ilimin ƙere-ƙere da fasahar na`u`rorin sadarwa da ci gaban masana`antu. Duk da haka yana da kyau a fahimci yadda al`umma ta ginu da yadda take gudanar da rayuwarta. Ta hanyar adabin baka za a iya fahimtar waɗannan abubuwa. Ashe abu ne mai muhimmanci a bayyana dalilan da suka sa ake buƙatar adabin baka. Wannan darasi zai wayar wa da ɗalibai kai kan muhimmancin adabin baka da yadda ake amfani da shi wajen gina tunani da kaifafa shi don a sami tsarin rayuwa mai inganci.

Ɗangambo, (2008:105) ya bayyana wasu manyan batutuwa, waɗanda ta nazarinsu ne, za a iya fahimtar muhimmancin adabi da nazarinsa ga rayuwar Bahaushe. Rarraba adabin Hausa kashi-kashi, zai taimaka wajen fahimtar rayuwar Bahaushe da kuma gano hanyoyin da za a inganta ta. A taƙaice, adabi da nazarinsa suna da wannan muhimmancin ga rayuwar Bahaushe:

1. Raya al'adu da inganta su; kuma nazarin adabi, zai fito da su fili a gane su.
2. Keɓe tarihin Bahaushe; adabi da nazarinsa, zai taimaka wajen adana tarihi, domin in an san jiya, an san yau, za a san yadda za a fuskanci gobe.
3. Tabbatar da, da kuma nuna martabar Bahaushe da ƙasa baki ɗaya. Kuma adabi, yana cusa alfahari da kai, sanin ciwon kai da kishin zuci da kishin ƙasa da kuma girmama abin da aka gada daga kakanni.
4. Zai taimaka a san rayuwar Bahaushe
5. Wasa ƙwaƙwalwa, ta bayyana abubuwan fasaha da lugga da sauransu.
6. Nasiha da gargaɗi da tarbiyya da koyarwa da hannunka- mai-sanda da sauransu.
7. Kyautata dangantaka da haɗin kai da girmama juna tsakanin al'umma da ƙasa da maƙwabta.

8. Nishaɗi da kore baƙin ciki da kewa da raha da makamantansu.
9. Bunƙasa ilimi da wayar da kai.
10. Koya dabarun zaman duniya, da ma amfanin lahira

Waɗannan, a taƙaice kenan, amma idan an faɗaɗa za iya samun manyan gidaje kamar haka: **gina tunani da kaifafa** shi da koyar da **tsarin rayuwa**.

### 1.4.1 Gina Tunani

Zantukan hikima da fasaha suna gina tunanin al`umma, ire-iren waɗannan zantukan hikima suna buƙatar wasa ƙwaƙwalwa wajen warware matsalar da aka gabatar. Don haka, neman warware matsalolinn kan sa a wasa ƙwaƙwalwa, ta haka ake samun mafita ga matsalar da aka gabatar, ire-iren waɗannan matsaloli suna tarbiyantar da al`umma ta yadda za su tunkari rayuwa musamman idan mutum ya ci karo da irin matsalar da aka bayyana a cikin adabin.

### Kaifafa Tunani

Idan tunani ya ginu, watau ilimin da zai zama tamkar fitila mai haskaka rayuwa ya samu, akwai kuma buƙatar a kaifafa shi. Abubuwan fasaha da ke damfare da adabin baka na bunƙasa ilimi da kaifafa shi. Ashe ba samun ilimi kaɗai shi ke da muhimmancin ba, har da yadda za a ci gaba da amfani da shi don wayar da kai da kuma al`umma baki ɗaya.

### 1.4.2 Koyar Da Tsarin Rayuwa

Sannannen abu ne cewa, mutanen da sun yi amfani da hikimomin adabin baka wajen koyar da tsarin rayuwa da yadda ake son jama`a su tarbiyantu da tsarin rayuwa, ɗaya daga cikin waɗannan hanyoyi ita ce tatsuniya, wadda aka ɗauka a matsayin makaranta ta farko wadda Bahaushe ya rinƙa amfani da ita wajen koyar da yaransa. Tatsuniyoyin Hausa suna koyar da yaran Hausawa kyawawan ɗabi’u da tarbiya ta hanyar nuna masu irin sakamakon da ke aukuwa ga wanda ba ya jin maganar iyayensa, misali, a tatsuniyar nan ta *Kura* inda ɗan auta ya ƙi bin maganar mahaifiyarsa, ya je ya soki tsuliyar zaki, zakin kuma ya zo ya halaka su. Haka kuma shi kansa zaman sauraron tatsuniya wata hikikima ce da Bahaushe yake amfani da ita don tarbiyan yaransa don kuwa yana hana su yawon banza da lalacewa da daddare (musamman ma ‘yan mata), maimakon a tafi dandali a yi wasa, sai a tara su a gida wuri guda ana yi masu wa’azi a kaikaice. Haka kuma Hausawa sukan sami abin annashuwa da ban dariya ta hanyar tatsuniya don kuwa akwai abubuwa da ake ƙirƙiro wa na ban dariya da mamaki ga mutane waɗanda babu yadda za a yi su iya aukuwa a halin rayuwa.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

| | |
|---|---|
| 1. | Bayyana ma'anar adabin baka tare da misalai masu kama hankali. |
| **2.** | Bayyana wasu daga cikin muhimmancin adabin baka. |

## 1.5 Taƙaitawa (Summary)

Daga bayanan da suka gabata, za a iya fahimtar cewa al`ummar baƙar fata na da hikomomi da fasahar da ta keɓanta gare su tun kafin su iya karatu da rubutu. Haka nan kuma, an fahimci cewa ci gaban al`umma ko ilimi ba sun rataya ga iya karatu da rubutu ne kawai ba. Kuma ma ai da yawa daga cikin waɗanda suka yi waɗannan rubuce-rubucen ba ƙwararrun nazarin adabi ba ne, don haka ba a yi mamaki ba in sun kasa gane fa`idar ko darajar adabin da suka tarar na al`ummar baƙar fata. Bayanan da ke sama sun gwada cewa adabin baka ba ƙashin yarwa ba ne wajen muhimmanci da saita tsarin zamantakewar al`umma. A taƙaice, adabin baka na gina tunani da kaifafa shi da kuma koyar da tsarin rayuwa yadda za a sami ci gaban alumma. An bayar da kaɗan daga cikin muhimmancin tatsuniya wadda ta kasance makaranta koyar da yaran alummar Hausawa.

## 1.7 Manazarta Da Waɗansu Abubawa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)


Ayindaho, K. (1985) "The Present State of African Literature Studies" In*African Literature Studies: The Present State*. Ed Stephen Arnold, Washington; African Literature Association & Three Continent's Press.

Babajo, A. K. (2011). *Orature: Meaning, Nature and Forms*. A Study Guide for Undergraduate, Kaduna: Slimline Communication.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Finnegan, R. (1970). *Oral Literature in Africa*. Oɗford: Oɗford Uniɓersity Press.

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Serɓices.

Gusau, S.M. (2006). Tatsuniya (Gatana) : Sigoginta da Hikimominta. Cikin*Mujallar Algaita*, 4,1.

Lorentzon, L. (2007). Is African Oral Literature Literature? *Research in African Literatures, 38*(3), 1-12. Retrieбed February 7, 2020, from www.jstor.org/stable/20109492

Okoh, Nkem. (2008). *Preface to Oral Literature,* Africana First PublishersLimited, Books House Trust, Onitsha Nigeria.

## 1.8 Amsoshin Tambayoyi

1. Adabin baka shi ne akasin na zamani. Shi ne adabin da ake ce masa adabin gargajiya. Ya shafi dabaru da hikimomin da Hausawa ke bi ta amfani da fatar baka domin ilimintar da yaransu. Ya kuma shafi siyasa da tattalin arziƙi da kuma kishin ƙasa.
2. Mihimman abubuwa na adabi suna nan kamar haka:

a. Waƙa/waƙoƙin gargajiya
b. Wasa/wasanni na zahiri
c. Tatsunia
d. Jarumta
**e.** Jajircewa

## Kashi Na 2 Rabe-Raben Adabin Baka: Waƙar Baka

### Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ma'anar Waƙar Baka
  2.3.1 Makaɗan Fada
  2.3.2 Makaɗan Jama'a
  2.3.3 Makaɗan Maza
  2.3.4 Makaɗan Mata
  2.3.5 Makaɗan Ban Dariya
2.4 Makaɗan Baka Na Zamani
2.5 Kayan Kiɗan Hausawa
2.6 Taƙaitawa
2.7 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.8 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.9 Amsoshin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa (Introduction)

A darasin da ya gabata, mun ga ma`anar adabin baka da manufarsa, a wannan kashi, za a yi bayanin muhimman rabe-raben adabin baka waɗanda suka haɗa da waƙar baka da zube na baka da kuma wasannin kwaikwayo na baka. Mu ɗauki waƙar baka, wato waƙar da ake ƙagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka. Za a tattauna musamman abin da ya shafi ma'anar waƙar baka da makaɗan baka, sai kuma ire-iren waƙar baka da kayan kiɗan Hausawa na gargajiya da na zamani. Sa`annan kuma kashin ya ƙunshi bayani kan turke da salo da tsarin waƙar baka. Za a tattauna musamman abin da ya shafi ma'ana da yadda turke da salo da tsari yake a waƙar baka.

### 2.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce koyar da waƙoƙin baka na baka na Hausa da ire-irensu. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma'anar waƙar baka da makaɗan baka
- Rarrabe waƙar baka da makaɗan baka
- Ire-iren makaɗan baka
- Fayyace nau'o'in da misalan kayan kiɗan Hausawa
- Ma'anar turke a waƙar baka da ire-irensa

- Rarrabe tsakanin salo da sarrafa harshe a waƙar baka
- Fayyace yadda tsari yake a waƙar baka

## 2.3 Ma’anar Waƙar Baka

Waƙoƙin baka kamar yadda sunansu ya nuna, su ne waƙoƙin da aka yi da baki, abin nufi a nan shi ne, su dai waƙoƙin baka shirya su ake yi a zuci, kuma a gabatar wa mutane da su ta hanyar rera su da baki. Tun ainihinsu ba a rubuce suke ba, kuma mawaƙan da suke tsara su, ba a rubuce suke tsara su ba, sun ɓullo da su ne ta hanyar rerawa da baki, wani lokaci tare da kiɗa, wani lokaci kuma babu, (Tsoho (1983 :1). Waƙoƙin baka sun ƙunshi waƙoƙin mata na aikace-aikacen cikin gida da waƙoƙin yara na dandali da waƙoƙin cikin tatsuniyoyi da kuma waƙoƙin makaɗa da mawaƙan Hausa na gargajiya.

Gusau (1984), ya bayyana waƙar baka da cewa ; “wani saƙo ne cikin zance da azanci da ake rerawa ba faɗa kurum ba, ta hikima da fasaha da zaɓaɓɓun kalmomi waɗanda suka dace da saƙon, kuma tana zuwa gunduwa-gunduwa da sautin murya da kiɗa da armashi da gaɗa da tafi mai saka zuciya jin daɗi.” (Gusau, 2008), ya ƙara da cewa akwai wasu matakai wato kalmomi muhimmai da za a iya amfani da su wajen fito da ma’anar waƙar baka, waɗannan kalmomi sun haɗa da rerawa da hawa da saukar murya da daidaita murya da rauji da naƙaltar harshe da hikima da fasaha da kiɗa da karɓi ko amshi.

### 2.3.2 Ma’anar Makaɗan Baka

Kafin bayyana ma’anar makaɗan baka, yana da muhimmanci a fahimci cewa waƙoƙin baka na Hausa akwai waɗanda ba a gwama su da kiɗa misali waƙoƙin raino ko na aikace-aikacen gida na mata ko waƙoƙin dandali. Su waɗannan waƙoƙi suna samun amo ne daga tafi ko sautin kayan aikace-aikacen da sauransu. Akwai kuma waƙoƙin baka na makaɗan baka waɗanda akae gwama su da amo na kiɗa da kayan kiɗa. Waɗannan kalmomi guda biyu, makaɗa+ baka, suna yin nuni ne dangane da mutanen da suke yin kiɗa da waƙa, amma da fatar baki. Ma’anar kiɗa a nan za ta iya zama yin waƙa tare da kaɗa ko buga wani abu mai ba da amo ko sauti. (Gusau, 2008:110).

## 2.4 Ire-Iren Makaɗan Baka

Ana iya karkasa makaɗan baka ko dai ta fuskar saƙonnin waƙoƙinsu ko ta fuskar kayan kiɗansu ko kuma ta fuskar waɗanda suke yi wa waƙoƙinsu. Idan aka yi la’akari da waɗanda makaɗan suke yi wa waƙoƙinsu, akwai makaɗan fada da makaɗan jama’a da makaɗan maza da makaɗan mata da makaɗan ban dariya da sauransu.

### 2.4.1 Makaɗan Fada

Makaɗan fada makaɗa ne suke waƙoƙin fada ko na sarauta. Irin waɗannan makaɗa ba sa yi wa kowa kiɗa da waƙa, in ba basarake ba. Akasarinsu suna da ubangida basarake wanda shi kaɗai suke yi wa kiɗa da waƙa. Ko da za su yi wa wani wanda ba ubangidansu ba waƙa, sai sun nemi izini daga iyayen gidan nasu. A taƙaice dai, makaɗan fada su ne waɗanda suke yi wa sarakuna da hakimai da dagatai da manayan fadawa da masu riƙe da sarautun gargajiya da duk wanda ya danganci jinin sarauta ko kuma yake riƙe da wani muƙami na sarauta waƙoƙi. (Gusau, 2008:138). Misalin makaɗan fada sun haɗa da, Alhaji Musa Ɗanƙwairo Maradun da Ibrahim Narambaɗa da Salihu Jankiɗi Sarkin Taushi da sauransu.

### 2.4.2 Makaɗan Jama'a

Makaɗan jama'a su ne makaɗan da suke yi wa kowa da kowa waƙa. Ire-iren waɗannan makaɗa suna yi wa kowa da kowa waƙa, walau sarki ko attajiri ko ma'aikata ko malamai ko jama'a gama-gari, da sauransu. Misalan makaɗan jama'a su ne Alhaji Mamman Shata Katsina da Alhaji Adamu Ɗan Maraya Jos da Hamza Caji da Garba Liyo da Ahmadu Doka da Alhaji Shehu Ajilo Ɗanguzuri da sauransu. Suna amfani da kayan kiɗa kamar kalangu da kuntigi da gurmi da goge da sauransu.

### 2.4.3 Makaɗan Maza

Makaɗan maza ko makaɗan jarunta su ne makaɗan da suke yi wa jaruntaka da jarumai kiɗa da waƙa. Waɗannan sun ƙunshi waƙoƙin ɓarayi da waƙoƙin yaƙi da waƙoƙin dambe da sauransu. Misalan makaɗan maza sun haɗa da Alhaji Muhammadu Gambo Fagada Mai Waƙar Ɓarayi da Ɗan'anace mawaƙin dambe da sauransu.

### 2.4.4 Makaɗan Mata

Makaɗan mata sun haɗa da kiɗan gaɗa da kiɗan shantu da kiɗan kalangu na saran marke da kiɗan duma wanda ake kaɗa wa samari da 'yan mata da kiɗan dutsi da kiɗan ƙwarya. Baya ga waɗannan kaɗe-kaɗe, akwai wasu mata da suka zama makaɗa waɗanda suke amfani da kiɗan ƙwarya da kiɗan ganga da kiɗan buta da kiɗan fiyano da makamantansu. Akwai kuma waƙoƙin mata maroƙa irin su Barmani Coge da Uwaliya Mai Amada da sauransu. Sauran Waƙoƙin Mata sun haɗa da waƙoƙin niƙa da waƙoƙin reno da waƙoƙin talla.

### 2.3.5 Makaɗan Ban Dariya

Makaɗan ban dariya su ne makaɗan da suke kiɗa da waƙa suna bayar da dariya ta hanyar kalamansu da shigarsu da yanayin waƙoƙin nasu. Ire-iren waɗannan makaɗan ban dariya sun haɗa da 'yan kama da 'yan gambara da sauransu. Makaɗan ban dariya sun haɗa da Malam Ashana Ɗankama da sauransu.

### 2.3.6 Makaɗan Baka Na Zamani

Tun kafin tasirin wasu baƙin al'ummomi kiɗa da waƙa ya samu gindin zama a al'ummar Hausawa. Daga baya ne zamani ya shigo da wasu abubuwa cikin waɗannan waƙoƙi na Hausawa (Gusau, 2012). An bayyana cewa a kafa ta waƙoƙin samartaka ne zamani ya shigo da tasirinsa a cikin waƙoƙin Hausa, wato waƙoƙin da samari da 'yammata ke yi (Gusau, 2008: 345-360). Waƙoƙin zamani sun kunno kai gadan-gadan ne a tsakiyar ƙarni na ashirin (Ƙ20) zuwa ƙarshensa, wato bayan yaƙin basasa, lokacin da ƙabilun kudanci Nijeriya suka yawaita (ɓarko) arewa da kuma yawaitar otel-otel a manyan garuruwan arewa. Tun a wajen shekara ta 1980 aka sami wasu makaɗa waɗanda suka dinga rera waƙoƙin Hausa ta amfani da kayan kiɗa baƙi. An sami makaɗa irin su Bala Miller da Fumi Adams da Audu Kwarisko da Sa'adu Bori da sauransu. (Gusau, 2008: 348).

A wajen shekara ta 1995 wasu Hausawa, musamman samari, suka fara tsara waƙa a rubuce sannan su samar mata rauji, su kuma rera ta amfani da kayan kiɗa baƙi. Wasu su haddace waƙoƙin da ka, wasu su ajiye su a kasa-kasai da CD – CD. Zuwa shekara ta 2000 jama'a ta fara sabawa da waɗannan kaɗe-kaɗe na fiyano da ake tsarmawa a cikin fina-finai. (Gusau, 2008:349). Yawancin irin waɗannan mawaƙa idan suka zo maimaita rera waƙoƙin suna bin rerawa ta farko ne daga CD wanda aka riga aka naɗa a sitidiyo, abin da ake kira '*Mamming*' da Ingilishi. Wannan kai tsaye tasiri ne baƙo wanda Hausawa suka samo shi daga tsari na naɗar waƙoƙin Turawa. Ga abin da Alan Waƙa yake cewa game da wannan:

> *"Baituka na zo in yi da kiɗa na Nasaranci,*
> *Kun ga na yi gurmi da kiɗa na Yahudanci,*
> *Baituka da sauti da salon masu Hausanci,*
> *Yakana na taso in gwada da badangalci,*
> *Ibrahimu za mu taya godiyar Allah."*
> (Aminu ALA: Waƙar Farfesa Malumfashi).

A yawancin lokuta, karin murya da saƙon iri ɗaya ne da na waƙoƙin Sa'in na asali, sai dai sukan bi wasu salo na zamani wajen tsara waƙar da kuma gwama su da kiɗa na zamani. (Mujaheed, 2018). Makaɗan

zamani sun ƙunshi Aminu Alan Waƙa da Adam A. Zango da Fati Nijar da Dauda Kahutu Rarara da sauransu.

## 2.4 Kayan Kiɗan Hausawa

Kiɗa abu ne da ake gwama abubuwa biyu su bayar da wani amo inda ake haɗa misali baki+ƙahon dabba, ko dutse+dutse, ko tafi+tafi, ko ganga + gula ko makaɗi da sauransu. Haka kuma duk da yake ana yin kiɗa don wata manufa, kiɗa yakan shiga jikin mai sauraro, ya sa masa karsashin da har za ta kai shi ya dinga rausayawa yana tattakawa. (Gusau 2008:54).

### 2.4.1 Ganguna

Su ne waɗanda ake kaɗawa da hannu ko ta amfani da gula wato ɗan makaɗi. Sun ƙunshi;

**2.4.2 Ganga-** Wannan babbar ganga ce wadda ake yi wa babban maratayi. Yawanci ana amfani da ganga wajen ƙiɗan noma ko na aikin gayya. Akan kuma sami wani nau'i na ganga ƙarama wadda wasu suke kira farar ganga.

**2.4.3 Kalangu-** Abin kiɗa ne wanda ake ratayawa a kafaɗa ana bugawa. Kalangu nau'i biyu ne: akwai babba da ƙarami. Ana iya kiɗa babban kalangu shi kaɗai ba tare da haɗa shi da wani abin kiɗa ba. Amma ƙaramin wanda ake kira kazagi ko kauzagi yakan zama mahaɗi ne na babban kalangu ko wani abin kiɗa kamar duma. Makaɗan sukan ɗaura shi a cinya yayin da suke buga babban abin kiɗa.

**2.4.4 Duman Girke-** Ana yin duman girke ne da duma manya da matsakaita masu bi wa juna a tsayi da faɗi. Ana kaɗa su domin a yi rawa kawai amma banda waƙa. Makaɗansu na jera su a gabansa ya riƙa bugawa. Kowannensu na bada sauti irin daban.

**2.4.5 Kotso-** Ƙaramar ganga ce. Sannan tsakiyar kotso a tsuke take, sa'annan kotso na da buɗaɗɗen baki domin ya ba da sauti mai zaƙi.

**2.4.6 Tambari-** Wannan babbar ganga ce mai shige da ƙwarya. Tambari ganga ce ta sarakai kawai. Hausawa sun samo ta ne daga al'ummar Barebari.

Sauran kayan kiɗa nau'in ganguna sun haɗa da:

| | |
|---|---|
| Turu | Jauje |
| Talle | Dundufa |
| Kurya | Banga |
| Zakka Tallabe | |
| Ƙoroso | bandiri/mandiri |
| Kwairama | Kuwaru |
| Duma | Cali |
| | TaushiKatsa, da sauransu |

**2.4.7 Kayan Bushe-Bushe**
Kayan busa su ne waɗanda ake amfani da su ta hanyar busawa, su ne:

**2.4.7.1 Algaita:** Algaita abin busa ne, saraki ake yi wa busar algaita.

**2.4.7.2 Farai:** Farai ma abin busa ne, kuma kamar algaita, farai kiɗan saraki ake yi da shi, tun ma ba Sarkin Musulmi ba.

**2.4.7.3 Ƙaho:** Ƙahon da aka fi amfani da shi wajen busa shi ne ƙahon saniya ko bajimin sa. Ana yi masa ƙofofi guda uku, ɗaya babba daga sama gefen dama, ɗaya kuma ƙarama daga gindinsa, da kuma wadda za a yanka daga tsakiya a dinga sa baki ana busawa. Ana tattaɓa sauran ƙofofin da hannu.

**2.4.7.4 Kakaki:** Kakaki abin busawa ne. Ana yin sa ne da ƙarfe mai kama da saholama. Nau'i biyu ne ƙarami marar faɗin ciki wanda za su yi wa ƙofa, da babba mai ɗan tsawo da faɗin ciki. Wani lokaci ma akan yi shi gaba uku yadda za a iya kakkarya shi. Daga nan, za a yi ƙofa ƙarama daga gindinsa (farko) inda za a sa baki a dinga busawa da ƙofa babba daga ƙarshensa wurin da sauti zai dinga fita.

Sauran kayan bushe-bushe sun ƙunshi:

| | |
|---|---|
| Sarewa | Damalgo |
| Ƙwabiri | Siriƙi |
| Kwagira | Kulema |
| BututuFamfami | |

Tilliɓeri Usur, da sauransu.

**2.5 Isga da Tsakiya**
Su ne waɗanda ake kaɗa su ta hanyar goga tsarkiya da ke jikinsu, misalansu;

**2.5.1 Goge:** Goge ana goga shi ne. Ana amfani da izgar doki wajen ƙulla abin da ake gogawa.

**2.5,2 Kukuma:** Kukuma kamar goge yake sai dai sautinta ba iri ɗaya yake da na goge ba.

**2.5.3 Garaya:** Wannan abin kiɗa ne da ake kaɗawa an fi amfani da garaya wajen kiɗan bori ko na iskoki.

**2.5.4 Kuntigi:** Kuntigi shi ma kaɗa shi ake yi amma girmansa bai kai na garaya ba.

**2.5.6 Gurmi:** Gurmi ya ɗara kuntigi tsawo, shi ma ana kaɗa shi ne kamar garaya ko kuntigi.

**2.5.7 Molo:** Molo ya yi kama da kuntigi ko garaya amma ya ɗara su girma. Shi ma kaɗa shi ake yi kuma ana haɗa shi da ƙoƙo da duma.

Wasu daga cikin kayan izga da tsarkiya sun haɗa da:

Kumsa
Kumbo
Gyanɗama, da sauransu.

## 2.6 Sauran Kayan Kiɗa

Wato kayan kiɗa da ba na bushe-bushe ba, ba kuma ganguna ba. Amma ana amfani da su wajen samar da amo na kiɗa. Ire-iren waɗannan kayan kiɗa sun haɗa da:

| | | |
|---|---|---|
| Shantu | Ruwan fartanya | Ɗuwawu |
| Kuje | Cekki | Ƙwarya |
| Buta | Zunguru | Saƙa |
| Barancaki | Tasa | da |
| sauransu | | |
| Kacau-kacau Gora | | |
| Sakaina | Madaɓi | |
| Zuga-Zugai | Dutsen niƙa | |
| Gwangwani | Turmi | |
| Akayau | Tafin hannu, da sauransu. | |

Sakaina Ƙwarya, ko Akayau.
Shantu ko Bambaro ko Barakaci.

### 2.6.1 Kayan Kida Na Zamani

Kayan kiɗa na zamani baƙi ne a ƙasar Hausa. Wato salon waƙoƙin zamanin ya haifar da samuwar kayan kiɗan zamani da suka haɗa da fiyano da jita da tasoshi da sauransu.

### 2.6.2 Turakun Waƙoƙin Baka

Makaɗa na shirya kalmomi su haɗa su da amon kiɗa su rera ta amfani da wani rauji tare da sakaɗa wani saƙo ko tuke domin isar wa al'umma (Gusau, 1993). Makaɗi kan yi kiɗa da waƙa mai ɗauke da saƙonni da dama.

Akwai fitattun saƙonni da za a iya ji ko hararowa daga waƙoƙin da makaɗan baka na Hausa suke shiryawa. Makaɗan suna kira da a riƙe al'adu masu kyau, sannan kuma suna ƙoƙarin dakushe marasa kyau. Daga cikin turaku na waƙoƙin baka, akwai;

1. Yabo: Makaɗan Hausa na faɗar kalmomi masu daɗi ga wanda ya aikata wani kyakkyawan abu. Ta yin haka suna fito da halaye da al'adun al'umma kyawawa. Wannan shi ne yaba hali, ko ɗabi'a na mutum ta nuna fara'ar mutum ko kyauta ko alheri ko adalci da rashin nuna bambanci tsakanin jama'a da sauransu. Misali, Shata ya yi wa Alhaji Sambajo waƙa ta yabo inda ya fito da halayensa kyawawa da alheri da kyautarsa. A cikinta yana cewa;

2.

Jagora: Ai ma fara'a ai ma alheri,
: kana a ja ka da wasan dangi,
: Je ka wurin Salisu Sambajo,

'Y/Amshi : Na gode wa Haji Sambajo.
Jagora: Kai mu je ko babu kiɗa ba waƙa,
: Mu zauna nan mu yi wasan dangi,
'Y/Amshi : Na gode wa Haji Sambajo.

3. Zuga: Zuga tana ɗauke da wasu kalmomi ne da ake amfani da su a koɗa wani mutum, a cicciɓa shi, a nuna fifikonsa kan wasu. Zuga takan tsuma mutum ta sa masa kuzari da ƙwarin gwiwa. A wajen zuga mutum akan yi amfani da kalmomin wasawa ko kumburawa ko ban tsoro ko cicciɓawa ko razanawa ko fifitawa ko naƙastawa da tauye zangon daraja da sauransu. (Gusau 2008:377). Misali

Allah ya yo ma ɗaukakad,
Da kowa ba shi da ita Hausa dut
(Ɗandawo: Sarkin Yawuri AbdullahiAbashi).

4. Zambo: Zambo kalma ce da ake amfani da ita a matsayin kishiyar yabo. Akan siffanta mutum da wasu siffofi munana waɗanda za su wulaƙanta shi ko su jawo masa rashin martaba a idon mutane, tare da kau da kai wannan mutum yana da waɗannan siffofi ko ba

shi da su. Akan ƙara gishiri a zambo don a daɗa lalata hali ko ɗabi'ar wanda ake yi wa shi. (Gusau 2008:380). Misali

To bismilla Allah ta'ala,
Ga farillin malan na baya,
Ga tarihin malam na baya,
Aura dillalin ƙuli-ƙuli
(Ɗanmaraya Jos: Karen Mota).

5. Faɗakarwa: Makaɗan Hausa, mutane ne waɗanda suke yi wa al'ummarsu faɗakarwa game da al'amuran rayuwa ta hanyar yi masu hannunka mai sanda da gargaɗi da tunasarwa da sauransu. Alhaji Mamman Shata Katsina ya yi wa mutanen Arewa gargaɗi da su tashi su nemi na kansu, su daina zaman banza da bacci domin ayyuka ne na lokaci. A wasu ɗiya ana cewa:

Jagora: Kai mai aski tsare askin naka,
: Mai tebur tsare kan teburinka,
: Mai akwaku tsare kayanka,
: Mai noma ka tsare gonarka,
: Ku turu mu farka ɗiyan Arewa,
: Ku san barci aikin kawai ne,
'Y/Amshi: Mu Tashi mu farka 'yan Arewa
: Mu san Barci aikin kawai ne.

Jagora: Kun ji ku tashi ku farka 'yan Arewa,
: Kowane aiki mutum yake yi,
'Y/Amshi: Mu tashi mu farka 'yan Arewa,
: Mu san barci aikin kawai ne.
(Shata: Waƙar Gargaɗi ga 'yan Arewa).

6. Ilmantarwa da Wayar da Kai: Makaɗan Hausa suna yin wasu waƙoƙi domin ilmantar da mutanensu da kuma wayar masu da kai kan wasu al'amura da ba su fahimta ba. Alal misali, a lokacin da aka sauya kuɗi a Nijeriya zuwa Naira da Kwabo. Makaɗa Haruna Uje ya yi waƙa don wayar wa al'umma kai game da sababbin kuɗin. Daga cikinta yana cewa;

Jagora: Naira da kwabo sabon kuɗi,
: Daɗa kun ji kuɗin Nijeriya,
: Allah ƙaro mana arziƙi,
: Gami da wadatar duniya.
Jagora: Idan ba ka san su ba,
: Jikin Naira Biyar,
: Fentinta da kore ɗan kaɗan,
: Kuma ka ga mutum guda.

Jagora: Da singileti wuya,
: Ka gane shi a durƙushe,
: Hannunsa akwai adda riƙe,
: Yana ta aikin kwakwan nan ta manja.
(Haruna Uji: Waƙar Naira da Kwabo).

7. Wa’azantarwa: Yawanci makaɗan baka, musamman na da, sukan yi waƙoƙi don yi wa al’umma wa’azi na horo da hani. Misali, Alhaji Mamman Shata Katsina ya yi wa mata wa’azi da su dinga yin aure. A wasu ɗiya na waƙar yana faɗin:

Jagora: Don Salla da salatil Fati,
: Albarkar girman mai girma,
‘Y/Amshi: Don Salla da Salatil Fati,
: Kai don Allah mata ku yi aure.

8. Siyasa: Siyasa hanya ce wadda ake amfani da hankali da lafazi mai daɗi a jawo ra’ayin mutane zuwa ga kyautata rayuwarsu. (Gusau, 2008). Yawancin waƙoƙin baka da aka shirya na siyasa sun danganci nuni kan kishin kai ko kishin ƙasa wani lokaci ma har da kishin addinin Musulunci. Wasu waƙoƙin kuma ana yi wa ‘yan siyasa ne. misalan waƙoƙin da suka danganci turken siyasa sun haɗa da;

- Babbar ƙasar Ɗanfodiyo Jamhuriyar Nijeriya.
(Ɗanharɗo Gumel: Kishin Ƙasa).

- Duniya ta yi kyau arziki ya yi,
Tun da mun karɓi ‘yanci cikin sa’a.
(Muhammadu Sarkin Taushi: ‘Yancin Arewa 1959)
(Gusau, 2008: 382).

9.Soyayya: Akwai waƙoƙin baka waɗanda suka jiɓinci turken saoyayya kamar waɗannan;

- Allah Sarki ya Allah,
Allah kai ni, Kaduna.
(Haruna Uji: Waƙar Jummai).

- Sai wata rana,
Habibu sai wata rana,
Na tuna da ran bankwananmu,
Habibu sai wata rana.
(Uwani Zakirai: Bankwana da Masoyi).
(Gusau, 2008: 383-384).

Waɗannan su ne muhimman turakun waƙoƙin baka na Hausa duk kuwa da akan sami wasu saƙonnin kamar na addini ko nishaɗantarwa ko ɗarsashin zuciya ko jaruntaka da sauransu da yawa.

## 2.7 Salon Waƙoƙin Baka

Salo dabara ce wadda ake kyautata harshen waƙa da ita tare da ƙawata zaren tunani ta yadda za a sarrafa shi cikin azanci ta zaɓen kalmomi ko sakaya furuci, a isar da saƙo wanda ake ginawa ta hanyar kaifafa tunani da balaga mai armashi. Ke nan, salo a waƙoƙin baka wata hanya ce wadda makaɗi ke kyautata zaren tunaninsa, ya sarrafa shi cikin azanci don ya cim ma burinsa na isar da saƙo a waƙa.

(Gusau, 2003:54). Ya ƙara da cewa salo a waƙoƙin baka abu ne wanda yake daɗa fito da ainihin kyansu ko muninsu, ta haka za a iya gane waƙoƙi masu karsashi, masu hikima da balaga da kuma waƙoƙi marasa ma'ana, marasa inganci. Salo kenan ma'auni ne na rarrabe zaƙin waƙa ko ɗacinta. Salo kuma hanya ce ta sarrafa harshe a jujjuya shi ta yadda za a iya taƙaita manufa ko a sakaya ma'ana ko kuma a kaifafa tunani.

### 2.7.1 Tsarin Waƙoƙin Baka

Gusau, (2003:32) ya bayyana tsarin waƙar baka a matsayin awon baka, inda ya ce a fagen nazari, ya shafi yadda makaɗi yake shirya waƙa a cikin zubin ɗiya da dabarun karin murya. Ya ƙara da cewa, a ɓanagaren ana duba zubin layuka da yawan ɗiyan waƙa da tsarin rerawa da karin murya da amsa-amon kari da sauran abubuwan da suka shafi awon baka. Ɗiyan waƙa kuwa tamkar rassa ne na itaciya wadda ake fara hawowa daga gindi kuma a sauka ta ƙasa. A kowane ɗa za a sami hawa da sauka. Ta haka ne mai nazari zai kula da yadda makaɗi ƙulla carbin tunaninsa da yadda yake saƙa kalmomi da saƙonni cikin jimlolibaki ɗaya (Gusau, 2003:33-34).

Kenan a iya cewa tsari a waƙar baka na bayyana Rukunin da mawaƙi ke amfani da shi wajen bayyana dangantakar da ke tsakanin ɗa da manufa wajen isar da saƙo ta amfani da salo mai gamsarwa wajen rera waƙoƙin.Da haka ne ma Satatima, (2009:127-128) ya ce: "tsari a nazarin waƙar baka shi ne fannin da ke fayyace ɗan waƙa a matsayinsa na ƙunshiyar saƙo ko manufa a cikin waƙa da ke bayyana yadda mawaƙi yake shirya tunaninsa wajen ƙulla kalmomi da jumloli su bayar da saƙon da yake burin isarwa ga al'umma (Satatima, 2009:127-128). Saboda haka, tsari a waƙar baka na bayyana Rukunin da mawaƙi ke amfani da shi wajen bayyana dangantakar da ke tsakanin ɗa da manufa wajen isar da saƙo ta amfani da salo mai gamsarwa wajen rera waƙoƙi. A dunƙule, tsari a waƙar baka shi ne hanyar da mawaƙi ya bi wajen jera tunaninsa

tare da shirya shi domin ya isar da saƙonsa ga mai sauraro.

### 2.7.2 Sarrafa Harshe a Waƙoƙin Baka

Muhammad (1973), ya bayyana cewa salon sarrafa harshen waƙa ya ƙunshi abubuwa ne kamar ƙarangiya da amsa-amo da ɗinkin baitoci da zambo da baƙin kalmomi da Hausantarwa da tsofaffin kalmomi da karin harshe da saɓi-zarce da kuma wasu ɓangarorin adon harshe kamar su kwalliya da tamka da mutuntawa da kamance da kuma siffantawa. Ɗangambo, (2007) ya ƙara da ginin jumla da kuma nau'o'in jumla, sai dai kuma shi ya kira sarrafa harshen waƙa da 'nahawun waƙa'.

A wani ƙaulin Gusau, (2003:62-63) ya nuna cewa dangane da aiwatar da harshe a nazarin waƙoƙin baka akan duba hanyoyin zaɓen kalmomi da karin harshen waƙa da kuma ginin jumla da tsarinta. Gusau, (2003:54), ya ci gaba da cewa za a iya karkasa salon sarrafa harshe zuwa gidaje biyu wato adon harshe da kuma aiwatar da harshe.

Shi kuwa Mukhtar, (2004), cewa ya yi, akwai wasu muhimman siffofi da mai nazarin salon sarrafa harshen waƙa ya kamata ya nazarta, waɗanda suka haɗa da na ginin kalma, da na ginin jumla da na tsarin sauti da kuma na adon harshe.

Garba, (2011:45-46) ya bayyana cewa; "Salon sarrafa harshen waƙa ya ƙunshi abubuwa masu yawa waɗanda suka haɗa da ƙarangiya da amsa-amo da tamka da mutuntarwa da kamance da ɗinki da zambo da kwalliya da baƙin kalmomi da Hausantarwa da karya dokar nahawu da karin harshe da saɓi-zarce da siffantawa. Sai a ƙara da sifar harshe wato ginin jimla da tsarinta da nau'o'inta." Kenan, armashin waƙa ko rashinta ya danganta da irin salon da mawaƙi ya yi amfani da shi wajen sarrafa harshensa.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

Amsa waɗannan tambayoyi **:**

1. Bayyana ma'anar waƙar baka da makaɗan baka
2. Kawo ire-iren makaɗan baka ka bayyana uku daga cikinsu tare da misalai.

## 2.8 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi an tattauna kan waƙar baka, wato waƙar da ake ƙagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka. An bayyana ma'anar waƙar baka da

makaɗan baka, sai kuma ire-iren makaɗan baka da kayan kiɗan Hausawa na gargajiya da na zamani. Sa`annan kuma kashin ya kawo bayani kan turke da salo da tsarin waƙar baka. An tattauna ma'ana da yadda turke da salo da tsari yake a waƙar baka.

## 2.9 Manazarta Da Waɗansu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)


Ɗangambo, A. (2007). *Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa*. Kaduna: Baraka Press and Publishers Limited.

Garba, S. (2011). "Salon Sarrafa Harshe A Waƙoƙin Aƙilu Aliyu". Kundin Digiri na Uku. Zariya: Sashen Harsuna Da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Gusau, S.M. (2008). *Waƙoƙin Baka A Ƙasar Hausa: Yanaye-Yanayensu Da Sigoginsu.* Kano: Benchmark Pulishers Limited.

Gusau, S.M. (2009). Diwanin Waƙoƙin Baka: Zaɓaɓɓun Matanoni Na Waƙoƙin Baka Na Hausa. Kano: Century Research and Publishing Limited.

Gusau, S. M. (2014) *Diwanin Waƙoƙin Baka.* Juzu'i Na Biyu: Century Research and Publishing Limited Kano-Nigeria.

Muhammad, Ɗ. (1978). "Waƙa Bahaushiya". cikin *Studies in Hausa Language, Literature And Culture*. Kano: Bayero Uniɓersity

Mujaheed, A. (2018). "Hankaka Mai Da Ɗan Wani Naka: Waƙoƙin Salisu Sa'in Makafin Zazzau a Bakin Mawaƙan Ƙarni na 21". *Kadaura: Journal of HausaMulti-Disciplinary Studies,* Ɓol. 1, No. 4, Special Edition. Department of Nigerian Languages and Linguistics, Kaduna State Uniɓersity-Nigeria.

Mukhtar, I. (2004). *Introduction To Stylistics Theories, Practice And Criticism*.Abuja; Country Side Publishers Ɓol. I.

Satatima, I.G.(2009). "Waƙoƙin Baka na Ɗarsashin Zuciya: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu." Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya (2013) *Makaɗi A Mahangar Manazarta:* Jerin Takardun da Aka Gabatar a Taron Ƙara wa Juna

Sani Kan Tubar Muhammadu Gambo Mai Kalangu, Gidan Dabino Publishers.

Tsoho, M.Y. (1983). "Waƙeƙeniya". Kundin Digiri na Ɗaya. Zariya: Sashen Harsunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

## 2.11 Amsoshin Tambayoyi

1. Waƙa tana nufin rairai zance cikin Magana da adon harshe zambo cikin zaƙin mirya. Makaɗan baka kuma su ne waɗanda suka bayyana kafin na zamani. Suna ɗauke da kayan kiɗa na gargajiya. Irin su molo da ganga da kalangu da shantu da dai sauran su.

2. Ire-iren makaɗa sun haɗa da:

a Makaɗan Fada
b makaɗan jama'a
c makaɗan maza
d makaɗan sha'awa
e. makaɗan ban-dariya.

- misali makaɗan maza su ne masu yi wa 'yan dambe da 'yan kokuwa da ɓarayi waƙa. Misali kamar Gambu Fakada da Ɗan'Anace da wasun su.
- misalan makaɗan sha'awa su ne ke wa kowa da koma waƙa. Misali suna waƙe tsuntsaye da yanayi da mutane. kamar irin su Haruna Oji da Hassan wayam da Mamman Barka da suran su.

## Kashi Na 3: Zube Na Baka

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Tatsuniya
3.4 Tarihihi
3.5 Ƙissa
3.6 Hikaya
3.7 Taƙaitawa
3.8 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.9 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.10 Amsoshin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa (Introduction)

Tun kafin haɗuwar Bahaushe da baƙi, yana da hanyoyi da dama da yake amfani da su domin ilimantar da kuma tarbiyantar da `ya`yansa ta yadda za su tashi cike da dabaru da kuma ilmin zamantakewa. Waɗannan hanyoyin kuwa su ne ire-iren labaran da ya tanadar waɗanda ake kira zube na baka, sun kuwa haɗa da maganganunsa na azanci da sauransu. Wannan kashi bayani ne kan zube na baka, wato zuben da ake ƙagawa a ka, a wanzar ta baka, a adana a ka, musamman abin da ya shafi dogayen labarun baka da suka haɗa da tatsuniya da hikaya da ƙissa da kuma tarihi da tarihihi.

### 3.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce koyar da zube na baka na Hausa musamman dogayen labarun baka. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Fasalce-fasalcen labarun baka na na zube
- Misalan zube na baka
- Bayyana muhimman nau’o’in zube na baka

### 3.3 Tatsuniya

Tatsuniya tana daga cikin manyan rasa na adabin bakan Bahaushe ɓangaren zube, kuma ƙagaggen labari ne da Bahaushe kan ba `ya`yansa

domin su tashi cikakku kuma kamillu. Gusau, (2006) cewa ya yi "tatsuniya wani tsararren labari ne wanda magabata (musamman tsofaffin mata) suke shiryawa cikin hikima da nuna ƙwarewa da naƙaltar harshe da ya ƙunshi wata shiryarwa da nuni zuwa ga halaye da ilmin zaman duniya, sannan da saka nishaɗi da raha ga rayuwa da kuma cinye dare".

Tun a farkon al`amari, Hausawa suna da labaransu na tatsuniyoyi waɗanda su ne suka ƙirƙiro su da kansu don nishaɗi da koyarwa. Sun mallaki wannan hanya ta bayyana matsayinsu, musamman ga yara, tun jimawa, ba sai da suka cuɗanya da wata al`umma ta koya masu ba. Hasali ma dai ba za a iya bugun gaba a ce ga lokacin da aka fara yin ta ba. Tatsuniya gadon gado ce, ta ginu a sakamakon tasirin al`adar rayuwa ta Hausawa, har ta zama ruwan dare game duniya (Yahya da wasu 1992). Haka kuma, labari ne ƙagagge ake harhaɗawa a tayar da gangar jikin tatsuniya, har a kaɗa ta, ta bayar da wani amo da ake son sadarwa ga masu saurare.

Saboda haka tatsuniya makaranta ce ta Bahaushe, ta nan yakan ilimantar da `ya`yansa dabarun zaman duniya tun kafin Bahaushe ya sadu da baƙi. Al`adun Hausawa ne suka haifar da tatsuniya kuma wajibi ne a yi la`akari da cewa tatsuniya ta samu tun kafin Bahaushe ya iya karatu da rubutu balle ya kafa makaranta. Tatsuniya ta wanzu cikin al`ummar Hausawa wadda tunaninta da hikimominta da fannonin ilminta duk da baki ne akan baza su, daga wannan mutum zuwa wancan da kuma wannan zamani zuwa wancan. Koyo da koyarwa, ɗabi`ar ɗan adam ce, saboda haka ya zama tilas ga Bahaushe ya ƙirƙiro wata hanya ta aikawa da hikimominsa da al`adunsa daga zamani zuwa zamani. Ɗaya daga cikin waɗannan hanyoyi ita ce tatsuniya. Ta amfani da tatsuniya Bahaushe kan kaifafa tunanin `ya`yansa.

### 3.3.2 Tarihihi

Asalin wannan kalma ta tarihihi an samo ta ne daga kalmar tarihi ta hanyar liƙa wa kalmar ɗafa-ƙeya na 'hi', sai ta koma 'tarihihi'. Sai dai abin kula a nan shi ne tarihi dai yana nufin wani labari ne na haƙiƙa da ya taɓa faruwa a cikin al'umma. To, amma shi tarihihi za a iya cewa, wani labari ne na wasu abubuwa da suka taɓa wakana na haƙiƙa a cikin al'umma, sai dai irin wannan labarin yana cakuɗe da wasu abubuwan da ba a tabbatar da faruwarsu ba. Don haka idan aka ce tarihihi, a taƙaice ana nufin gurɓataccen tarihi, wanda aka cakuɗa shi, a tsakanin gaskiya da ƙarya.

Tarihihi, labari ne da ake riƙe shi da ka, kuma kasancewar kai ba mariƙi ba ne, ballantana har ya yi ajiya, sai wajen ruwaito waɗannan abubuwa da suka faru a rayuwa ake gwama su da waɗanda ba su faru ba, wato dai

yawancin tarihihi, ya ƙunshi labarai ne na kunne ya girmi kaka, waɗanda ba a iya tabbatar da haƙiƙanin aukuwarsu ba. Kuma labarai ne da suka ƙunshi abubuwan da suka danganci rayuwar Hausawa, musamman a jiya. Akwai tarihihi kala-kala a ƙasar Hausa sai dai waɗanda suka yi tashe sun haɗa da na taririhin Bayajidda da tarihihin sarkin Katsina Korau da tarihihin Wali Ɗanmarina da Wali Ɗan Masani ko wani ɓangaren tarihin Usman Ɗanfodiyo ko Ɗanwaire da makamantan su.

### 3.3.3 Ƙissa

Ƙissa kalma ce da aka samo daga harshen Larabci wadda ta shige tsundum a cikin adabin Hausa. Ita dai wannan kalma tana ɗauke da ma'anoni biyu ne a cikin harshen Larabci. Wato ma'ana ta lugga da kuma ta zahiri. A luggance, ƙissa na nufin bibiya ko ƙididdigewa. Watau mutum ya bi diddigin wani abu har ya zuwa ƙarshensa.

A ma'ana ta zahiri kuwa, kalmar ƙissa na nufin bada labarai dangane da mutanen da suka shuɗe, ko kuma bada labarai a kan waɗansu abubuwa da suka auku a da. Ko kuma wani labari da ke kara zube da ya ƙunshi shiryarwa zuwa ga addini ko gaskiya ko neman tsira kan wani abu. A ra'ayin masana da dama sun yi nuni da cewa an fi danganta ma'ana da manufar ƙissa a kan labarun da suka danganci addini kawai. Watau bayanai a kan rayuwar annabawa da sahabbai da waliyyai da sauran su. Duk da haka akwai wasu labarai na ƙayatarwa da jawo hankali da za a iya kiran su da ƙissa, kamar irin ƙissoshin da suka shafi soyayya. Don haka akan ce ƙissa wata hanya ce ta cusa wata manufa cikin zukatan masu saurare.

Duk da irin wannan hasashe game da ƙissa ana da fahimtar cewa ta shafi abin da ya bibiyo labarin annabawa kamar yadda ya zo cikin Alƙur'ani mai girma, inda ake da surori da suka bayyana labaran annabawa da aka zayyana a cikin Al'ƙur'ani. Sai dai ita ƙissar da Bahaushe ke bayani ta shafi wadda aka gina ne bisa tunanin Bahaushe, wato ga yadda labarin yake a zahiri amma a ƙara masa wani abu ko dai don daɗin labarin ko kuma domin a ƙara ƙayatar da mai sauraro. Alal misali ƙissar Annabi Yusuf ko ta Annabi Sulaiman ko kuma ta Annabi Nuhu za a same su da ɗan bambanci da wadda ƙur'ani ya zo da ita. Shi ya sa masana suka raba ƙissar zuwa gida biyu:

i) Ƙissar Cinye Dare: Wadda ta ƙunshi labarai da zantuttukan da mutane suke yi don cinye dare.
ii) Ƙissar Addini: Wannan ta ƙunshi labarai ne da ake tsarawa a kan wani abu da ya auku na addini a lokacin annabawa da sahabbai da waliyyai da shaihunnai da sauran su.

A Hausance ke nan, ƙissa labari ne na gaskiya da aka bayar ko ake bayarwa a kan rayuwar annabawa da sahabbai ko waliyyai ko shaihunnan malamai, ko wasu bayin Allah da sauran su da suka danganci addinin Musulunci, musamman waɗanda Alƙur'ani da Hadisai suka kawo bayaninsu. Hausawa sun sami damar sanin wani labari da ake kira da suna 'ƙissa' bayan cuɗanyarsu da Larabawa, suka kuma samu damar rabauta da addinin Musulunci. Don haka a iya cewa tasirin addinin Musulunci da karance-karancen da suka danganci tafsiri da hadisai da wa'azi wajen watsa addinin Musulunci, su ne suka taimaka wajen samuwar ƙissa a al'ummar Hausawa. Masana da dama sun raba ƙissa zuwa sassa daban-daban. Daga cikin su akwai Sa'idu Muhammad Gusau wanda ya kasa ƙissa zuwa nau'i huɗu kamar haka:

- Ƙissar Annabawa, wadda ta bayyana rayuwarsu ta haƙiƙa da irin gwagwarmayar da suka sha wajen isar da saƙon Ubangiji (Allah).
- Ƙissar Sahabbai da waliyyai da shaihunnai, wadda ke ƙunshe da bayanin rayuwarsu.
- Ƙissar sauran bayin Allah (muminai), wadda take bayyana rayuwar wasu bayin Allah, nagartattu da suka miƙa wuyansu ga addinin Allah.
- Ƙissar kangararru, waɗanda suka bijire wa addinin Allah.

### 3.3.4 Hikaya

Hikaya labari ne da ake ba da wa da ya faru dangane da mala`iku, ko aljannu ko mutane ko rauhanai ko dabbobi ko tsuntsaye ko kuma ƙwari. Wani lokaci kuma takan ɗauki yanayin ƙago wasu labaran don ƙarin bayani kan wani abu ko kwaikwayon sa. Hikaya labari na manyan mutane, ba annabawa ba, da abin da ya faru gare su. Misali, hikayar wani halifa ko sahabi ko wani babban sarki. Hikaya kuma, takan ƙunshi wani abin mamaki da ya auku ko kuma dai wani labari mai koya darasi gaz aman duniya (ko ma amfanin lahira). Hikaya kuma tana iya zama ta wani attajiri ko kuma dai wani labari mai koya zaman duniya dangane da yadda mutum zai iya bakinsa, (Ɗangambo, 2008). Misali, Hikayar Kunkuru Da Gauraki :

Wata' rana, wasu gauraki guda biyu, za su yi balaguro sai wani kunkuru abokinsu ya roƙe su, su tafi da shi. Suka ce masa shi da ba shi da fuffuke ta yaya za su yi tafiya tare ? Amma sai ya nace sai ya sun tafi da shi. Shi kenan, sai suka yi dabara, suka ɗauko wata sanda kowace tsuntsuwa (gauraki) ta kama gefen sandar guda, shi kuma kunkuru ya riƙe sandar da bakinsa, suka tashi da shi. Suna cikin tafiya a sama sai suka ga wani abin dariya na aukuwa a wani gari da suka zo wucewa. Sai ɗaya daga cikin gaurakin ta ce ; "La, kin ga wani abin dariya, zomo na korar akuya." Ko da 'yar'uwarta ta duba ta ga haka sai ta ƙyalƙyale da dariya. Da kunkuru ya ji suna dariya, sai ya buɗe baki wai zai tambaye su abin

da ya sa suke dariya. Buɗe bakinsa ke da wuya, sai ya sullo, ya faɗo ƙasa ya farfashe. (Wai shi ya sa ake ganin bayan kunkuru duk a tsattsage). Wannan hikaya tana koya wa mutum ya iya bakinsa, domin kuwa da kunkuru ya iya bakinsa da haka ba ta faru da shi ba.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana ma'anar zube na baka da ƙirƙirarrun labarai
2. Bayyana ma'anar uku daga cikin waɗannan :
   i. Hikaya
   ii. Ƙissa
   iii. Tarihi Da Tarihihi
   Tatsuniya

## 3.5 Taƙaitawa (Summary)

Wannan kashi ya ƙunshi bayani ne a kan zube na baka, musamman abin da ya shafi labarun baka. An tattauna ma'anar zube da kuma ma'anoni na wasu daga cikin misalansu da suka haɗa da tatsuniya da hikaya da ƙissa da kuma tarihi da tarihihi.

## 3.6 Manazarta Da Waɗansu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : AmanaPublishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Serƃices.

Gusau, S.M. (2006). Tatsuniya (Gatana) : Sigoginta da Hikimominta. Cikin *Mujallar Algaita*, 4,1.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyi

1. Zube rubutu da ake yin sa a kan wani batu ko al’amari da ya kasance. Rubutun zube kamar yadda sunan ya nuna, ya bambanta da rubutun waƙa da na wasan kwaikwaiyo. Rubutu ne da ake yin sa sakin layi bayan sakin layi

2. a tarihihi labari ne wanda ya gabata. Sai dai ya sha bamban da tarihi. Domin shi tarihihi akwai ƙarin gishiri a ciki. Ma’ana ana samun ƙarin wani abu da ba gaskiya ba a cikin tarihihi. Za mu iya cewa, bai samu amincewa a wurin masana kufai ba, kamar yadda suka aminta da tarihi.

## Kashi Na 4 Wasan Kwaikwayo Na Baka

### Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Ma'anar Wasan Tashe
 4.3.1 Samuwar WasanTashe
 4.3.2 Ire-Iren Wasannin Tashe
 4.3.3 Ma'anar 'Yan Kamanci
 4.3.4 Yadda Suke Gudanar da wasansu
 4.3.5 Siffofin Kwaikwayo
4.4 Ma'anar Wasan Gauta
 4.4.1 Ire-Iren Wasan Gauta
 4.4.2 Lokacin da Yadda Ake Aiwatar da Wasannin
4.5 Taƙaitawa
4.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.7 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

### 4.1 Gabatarwa (Introduction)

Wasannin da ake magana a wannan kashi, wasanni ne da ake wanzar da su ta baka, wato ta hanyar nuna gwanintar harshe, akwai wasu daga ciki waɗanda ke buƙatar motsi da gaɓuɓɓan jiki sa`annan wasu daga cikin nau`in adabin baka su biyo baya, irin waɗannan sun haɗa da tashe da `yan kamanci.

### 4.2 Manufar Darasai (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce koyar da wasu daga cikin wasannin kwaikwayo na gargajiya waɗanda ake yin su da baki kuma suna ɗauke da ɓwasu sifffofi na adabin baka na Hausa. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma`ana da ire-iren wasannin tashe
- Ma`ana da yadda `yan kama suke da matsayinsu a al`ummar Hausawa.
- Yadda ake aiwatar da wasan gauta da kuma irin fai`dojin dake da ke tattare da waɗannan wasanni.

## 4.3 Ma’anar Wasan Tashe

Masana da dama sun bayyana ma`anar tashe da asalinsa, Ahmed, (1985:8) ya ce:
Tashe a kowane bangaren ƙasar Hausa ana yin shi ne a watan azumi, lokacin watan ya kai kwana goma abubuwa guda uku ne, na farko a tashi jama’a lokacin sahur, kamar yadda kalmar nan “tashe” ta nuna. Dalili na biyu shi ne, don hana mutane wasanni almubazzaranci, na uku ana yin wasannin tashe ne domin nishaɗi bayan buɗe baki’.

Shi kuma Umar (1980 :3) ya ce: ‘tashe al’ada ce da aka yi a cikin watan nan mai alfarma wato watan Ramalan. A wannan wata Ubangiji Tabaraka Wata’ala ya umarci Musulmi da yin azumi, ya kuma kwaɗaitar da su ga yawaita ayyukan Ibada.

### 4.3.2 Samuwar Wasan Tashe

Babu wani takamaimai lokaci da aka fara tashe, duk da haka, Musulunci ya zo da azumi a matsayin shika-shikansa, a saboda haka ne Bahaushe ya }ir}iri tashin mutane domin yin Sahur. Ana kyautata zaton daga wannan ɗabi’a ta tashin mutane domin su yi sahur saboda muhimmancin yin haka daga Alku’ani da hadisan Annabi (SAW) suka fa]i kamar haka: “yin sahur ba wajibi ba ne, amma dai sunna ce mai }arfi domin Manzon Allah (SAW) ya ce, bambancin azuminmu da na Yahudawa da na Nasara shi ne yin sahur wato abinci, ruwa ko dabino mutum ya samu ya ci” Muslim ya ruwaito.

Haka kuma, “yin sahur ko da ƙalilan ne akwai rahama a cikinsa a wannan lokaci” Bukhari da Muslim suka ruwaito. Abu Sa’eed Alkudri (RA) ya ce, ya ji daga Manzon Allah (SAW) ya ce “yin sahur ko da ɗan ruwa kaɗan ne shi yafi, kuma Allah Ya ka saukar da Mala’iku da su yi wa mai yin sahur addu’a. haka kuma Zaid Ibn Tabit ya ce mun yi sahur da ma’aikin Allah (SAW) sa’annan ya mie domin yin sallah, muka tambaye shi, menene bambancin lokaci tsakanin sahur da kiran sallah? Sai ya amsa da cewa wannan lokaci, zai ɗauki mutum ya karanci surori hamsin na Alkur’ani mai girma; Bukhari da Muslim suka ruwaito. Yin sahur na samun sau}in azumi, shi ya sa aka ri}a samun mutane wa]anda suka azawa kansu wannan nauyin aiwatar da wannan aiki ba tare da biyansu wata lada ba. Haka kuma ana ganin kalmar tashe wadda aka sani a yanzu ta samo asali ne daga wancan kalmar ta ‘tashi’, tashin jama’a da ake yi domin yin sahur.

### 4.4 Ire-Iren Wasannin Tashe

Dangane da ire-iren tashe, masana ilimi irin su U.B. Ahmed da Mallam M.B. Umar sun karkasa tashe na yara maza da zalla da tashen ‘yan mata da kuma tashen Samari matasa.

- **Tashen yara maza, sun haɗa da:** Sakanni-in [iba, ka-yi -rawa, [andu {ununu, Tsoho da gemu, Danda dokin kara, zan buga, kar-ka buga tashi wali da sauransu.
- **Tashen yan mata sun haɗa da:** Samodara, Maryama da Daudu, Asha ruwa, Mai ciki, Auren-gidan- ba-sharu-ba dadI da sauransu.
- **Tashen Samari:** Sun haɗa da Amale mai Jan-kaya, Jatau mai magani, gwauro ya tsinke, kai ni chadi zan tafi, macukule da sauransu.

### 4.5 Ma’anar ‘Yan Kamanci

`Yankama maroƙa ne da suka shahara wajen ban dariya das a mutane nishaɗi, Yahaya da Suwaid, (1978). `Yan kama masu wasannin ne na Hausa waɗanda suka yi kama da `yan gambara ko kuma Na-Uwale ko Ɗanbashirwa. Galibi kasuwanni suke bi suna wasanninsu ana basu abin masarufi. `Yan kama kan yi shiga suna kiɗa suna amfani da takobinsu na ice wajen kai suka domin su tsorata mutum ko don a yi dariya.

#### 4.5.1 Yadda Suke Gudanar da wasansu

Ahmed, (1985) ya yi cikakken bayanin yadda ɗankama ke gudanar da wasansa. Shi dai ɗankama ya kan sa buje ne, da babban riga. Amma fa rigar yakan kwaɓe ta ne ya yi ƙunzugu da ita a mararsa, watau ya bar gangar jikinsa a buɗe. Wasu kayan ‘ɗankama’ kuma su ne takobin ice da tasbahar ƙuliƙuli da garmar sakaina. Duk batun ɗankama dai bay a wuce ta abinci. Duk da yake ɗankama yakan faye ambaton addini musulunci, lamurar addinin nan yakan sake masu kama ne, ya mayar da ginshiƙinsu ya zan abinci.

- **Misalan Waƙoƙin Ɗan Kama**

Ɗan kama, gwani ne na kwaikwayo. Don haka, yakan kwaikwayi waƙoƙin makaɗa da yawa. Misali, ‘yan kama, suna kwaikwayi waƙoƙin sojoji a yaƙin Ojukwu inda sukan ce:

Kanar ɗan wake ya gudu,
Manjo fura ma ta gudu,
Janar funkaso ya gudu,
Mun ci fanke, mun ci waina,
Ƙaryar tuwo ta ƙare!

Haka kuma, sun kwaikwayi waƙoƙin Shata da yawa. Misali, inda suka kwaikwayi waƙarsa ta "Mata ku yi aure" suna cewa:
Don na ce mata su yi koko,
Masu kunu suka tozarta ni,
Har Attaura har Linjila,
Shin ina ayar da ta kankare koko?
A maimakon inda Shata yake cewa:
Wai don na ce mata su yi aure,
Kaɗo ya tashi ya tozarta ni,
Har Attaura har Linjila,
Har Alkur'ani babban kundi,
Ina ayar da ta kankare aure?

Haka kuma wani ɗan kama, wai shi Isa Rogo, ya buɗe wata tashar rediyo, wai ita Rediyo Mai Jini, inda yake kwaikwayon yadda ake ba da labarai a rediyo, Ɗangambo, (2008). Ga labarin yadda wani ɗan kama ya yi limanci:

- **Limancin Ɗan Kama**

Wai wata rana, wasu 'yan kama guda biyu, suka ziyarci wani gari, suka je fadar Sarki, aka yi musu iso. Da sarki ya gan su, sai ya yi zaton wasu manyan baƙin malamai ne. Da azahar ta yi, aka je masallaci don yin salla. Limamin garin, ya ga yadda sarki ya karɓi baƙin. Don haka, sai ya ce da ɗaya daga cikin 'yan kaman nan, "Malam, bisimilla. Ai, sai a yi mana salla." kuma don yana tsoron kada malaman su ci gyaransa a gaban sarki, shi ya sa ya yi haka. Ɗan kama ya wuce gaba yin salla.'Aka yi salla har sai da aka je sujada ta ƙarshe, sai ɗan kama ya ƙi tasowa. Mutane suka ƙosa. Zuwa can sai ɗan kama ya fara mutsu-mutsu, goshinsa na kafe a ƙasa. Sai ya fara cewa, "Ku sake ni! Wayyo ku sake ni! Ihu! Sun riƙe mini goslii!" Ko da jama'a suka ji haka, sai kowa ya tashi a tsorace, rididididi, in ba ka yi, ban wuri, tun daga Sarkin har limamin garin. Da 'yan kama suka ga an tsorata, sai suka zaro gangarsu, suna kaɗawa. Haushi ya kama mutane. Suka gargaɗe su cewa, bai kamata a kawo shaƙiyanci a masallaci ba.

Haka kuma, aka ce, wata rana, wani ɗan kama ya ziyarci wani ofis na wani babban ma'aikaci. Da ya je, ya sami wani masinja a ƙofar. Da masinjan ya gan shi, sai ya yi zato shi ma ya zo yin mitin ɗin da ake yi ne a cikin ofis. Don haka, sai ya miƙe tsaye, ya gaishe shi, ya buɗe masa ƙofa. Ɗan kama ya shiga. Ya sami mutane zazzaune kewaye da tebur da fayiloli. Ko da suka gan shi, sai suka rasa abin da ya kawo shi, domin ba su san shi ba. shi kuma ga shi cikin kaya masu kwarjini da muƙami. Don haka, sai wannan ya kalli wannan, wancan ya kalli wancan. Zuwa can dai, sai ɗan kaman ya ce, "Shin wane ne babbanku?" Ya zazzaro idanu. Da ya ga sun tsorata, sai ya yi wuf ya zaro takobinsa na akwasa, ya sake

cewa, "Na ce wane ne babbanku?" Sai ya ga duk suna kallon shugaban, wato Cayaman. Sai ko ya doshi wurinsa da takobinsa a zare, yana zazzare idanu. Da suka ga haka, duk sai suka tashi a guje rididdidi, a tsorace. Da ya ga haka, sai ya zaro gangarsa ya buga. Da suka gane ɗan kama ne, sai suka dawo cikin fushi, amma kuma abin ban-dariya, suka gargaɗe shi ya daina irin wannan, Ɗangambo, (2008).

### 4.5.1 Siffofin Kwaikwayo

Siffofin kwaikwayon da ke tattare da wasan ɗankama sun haɗa da yadda yake kwaikwayon yaƙi da kai bara a sukwane ga abokin gabansa ta hanyar yin amfani da takobin ice. A nan takobin iccen shi ne kwatakwacin takobi na zahiri, haka nan mutumin day a nufa da wannan takobi shi ne tamkar abokin hamayyarsa a fagen fama. Idan kuma yana son ya kwaikwayi `yan hoto, wat masu Nakiya-da Garma', ɗan kama kan yi amfani da garmarsa ta sakaina yana jefa ta sama yana kamawa. Wani muhimmin abu kuma idan yana son nuna bajinta bay a karɓan sadaka da hannu, sai dai a jefa masa shi kuma ya café da baki tamkar dai wata dabba mara hannu.

## 4.6 Ma'anar Wasan Gauta

Kamar yadda aka ambata a baya, *Wasan Gauta* wasan kwaikwayo ne wanda ake yi a fada da kuma wanda talakawa ke shiryawa su gudanar a dandali na musamman, asali abin da aka sani da suna Drama ana kiransa 'Gauta' ne, Yahaya da Suwaid, (1978).

### 4.6.1 Ire-Iren Wasan Gauta

Wasan Gauta iri biyu ne, da wanda ake yi fada da kuma wanda talakawa ke yi a cikin gari. Wanda ake yi a fada, {wara}waran sarki ke yin wasan. Sukan aika a kar~o masu suturu da kayayyakin ado na hakiman da za su kwaikwaya. Kowace baiwa takan nazarci shiga da halayyar hakimin da za ta kwaikwaya tun kafin lokacin wasan, kuma a lokacin gudanar da wasan ne su hakimai da iyalansu kan kasance 'yan kallo masu ganin hoton yadda suke gudanar da mulki da harkokin jama'a. Suna lura da yadda ake kwatanta halayyarsu da ɗabi'unsu da yadda suke tunkarar abubuwan da suka shafi al'umma. Ta wannan hanya ce suke fahimtar wuraren da suke da gyara kuma su gyara da wuraren da suke buƙatar ƙara himma don kare lafiyar al'umma da dukiyoyinsu.

Idan aka dubi wasannin da yadda ake gudanar da su sai a ga cewa suna nuna yadda Bahaushe yake yi wa kansa hisabi game da abubuwan da suka shafi mulki. Ta hanyar wasannin ne ake gane abubuwan da aka aikata. Idan masu kyau ne a ƙara himma, idan kuwa munana ne, a nemi hanyar kaucewar aukuwar irinsu. Ana ƙara himma wajen aikata

abubuwan da za su taimaka wajen tabbatar da adalci da tsaro da kyautata zamantakewa tsakanin al’umma. Mahukunta na yunƙurin sauke nauyin da Allah ya ɗora masu ta hanyar bayar da haƙƙoƙin da suka rataya a kansu. Suna kasance wa masu yayyafi da rangwame da lulluɓe al’ummarsu da abubuwan alheri. Suna basu kariya da ƙarfafa tsaron ƙasa da bunƙasa tattalin arziƙi da cinikayya ta sanadiyyar waɗannan wasannin.

Ɗaya ɓangare na Wasan Gauta shi ne wanda samari da ‘yan mata ke aiwatarwa a Dandali. ‘Yan wasan kan kwaikwayi halaye da ɗabi’un mahukunta ko da kuwa mahukuntar nan na ƙungiyoyi ne ko na al’umma. Akan bayyana wasu munanan halaye da ɗabi’u waɗanda suke neman kunno wa cikin al’umma, ana nuna yadda suke da illarsu ta hanyar wasa. Haka ma ta hanyar kwaikwayo akan nuna wasu halaye da ɗabi’un mutane marasa kyau, ko wani aikin ashsha ko sakaci ko raggwanci da wani ya yi domin masu aikata wannan aikin su gani su daina. Ya kuma zame wa sauran al’umma hannunka-mai-sanda. Wasannin kan ƙarfafa aikin gayya da jaruntaka da girmamawa da tausayin marasa ƙarfi da dogaro da kai. Mutane daga ko ina kan halarci wurin domin kallon wannan wasa, hatta baƙi ma daga {auyuka maƙwabta kan yi tafiya takakka domin halartar wasan.

### 4.6.2 Lokacin da Yadda Ake Aiwatar da Wasannin

Galibi da kaka ne aka fi aiwatar da wasan gauta idan an gama girbe amfanin gona, irin wannan wasa shi wasu ke kira Kalankuwa. Wasu lokutan da ake aiwatar da wasannin sun dogara ne ga irin wasan.

**AUNA FAHIMTA**

1. Shin ko an yarda da ƙirarin nan da ke nuna cewa Bahaushe ba shi da wasan tashe sai da musulunci ya zo ƙasar Hausa?
2. ‘Yan kama da `yan gambara kusan ɗan ne da Ɗan Jummai. Bayyan yadda abin yake tare da misalai.

## 4.7 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi an tattauna a kan wasannin Hausa masu siffar kwaikwayo ko kuma waɗanda suke cike da adabin baka kamar su waƙoƙi da hikimomin sarrafa harshe. Kashin ya ƙunshi bayanai kan ma’anar tashe da `Yan kama da kuma Wasan Gauta.

## 4.8 Manazarta Da Waɗansu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

Ahmed, U.B (198 5) *Nau'o'in wasannin kwaikwayon Hausa.* Cibiyar Nazarin Al'adun Nijeriya. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Muhammad, S. da Yahaya, I.Y (1978) *Darussa Akan Adabin Hausa.* Zaria. Institute of Education, Ahmadu Bello Uniɓersity.

Ibrahim, M.S (1982) "Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci Kan

Rayuwar Hausawa ta Gargijiya". Kano. Kundin Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero.

## 4.9 Amsoshin Tambayoyi

**1.** tabbas Bahushe bai san tashe kafin bayyana ddinin Musulunci a duniyarsa. Saboda babu w ani lokaci da Hausawa ke yin tashe sai a watan Ramalana idan ya kwana ashirin. Azumi kuma Addinin Musulunci ne ya zo da shi ƙasar Hausa. Da a ce akwai wani lokaci da ake tashe ba lokacin azumi ba, sai a iya cewa, Musulunci ya iske Bahaushe da al'adarsa ta tashe.

2. ‘Yan kama da ‘yan gambara duk dodo ɗaya suke ma tsafi. Domin gaba ɗayansu suna kwaikwayo wani abu ne ko mai rai ko marar rai su alaƙanta shi da duk abin ya zo musu a rai. Idan k aba sun a goro, sai su yabe ka su alaƙanta ka da jarumta ko ilimi. Idan kuwa k aba su haƙuri sai su muzanta ka. Ko su kushe halittarka ko kuma su alaƙanta ka da wani mugun abu. Kamar dabba jaki mai ƙaton kai da sauran su.

## Rukuni Na 2 Siffofin Adabin Baka

Kashi Na 1 Siffa
Kashi Na 2 Harshe
Kashi Na 3 Wanzarwa
Kashi Na 4 Saurare

### Kashi Na 1: Siffa

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma'anar Siffa
1.4 Jigo
1.5 Salo
1.6 Zubi
1.7 Taƙaitawa
1.8 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.9 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.10 Amshoshin Auna Fahimta

### 1.1 Gabatarwa (Introduction)

A wannan kashi, za a bayyana sifofin da suke tattare da adabin baka. Su waɗannan sifofi, ba dole a same su duka a nau`in adabin baka guda ba. Galibi ma kusan kowane yanki yana da tasa hanyar ko kuma abubuwan da aka fi amfani da su yayin da ake nazartar wannan rukunin adabin. Akwai muhimman gidaje guda uku waɗanda ke cikin adabin baka, waɗannan gidaje sun haɗa da **Waƙar Baka** da **Zube Na Baka** da kuma **Wasan Kwaikwayo**. Waɗannan gidaje (wa}a da zube da wasan kwaikwayo) duk ana samunsu a rubutaccen adabi. Saboda haka sifofin da aka yi bayaninsu a nan, suna magana akan kowane yanki na adabi walau adabin baka ko rubutacce.

### 1.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Ko shakka Babu wannan darasi na da manufofin da ake fatar ɗalibai su fahimta. A san ma`anoni siffofin da kuma yadda ake amfani da su wajen nazartar ayyukan adabi. A fahinci cewa waɗannan siffofin su ake nazarta a rubutaccen adabi.

## 1.3 Ma'anar Siffa

Siffa kamar yadda masana suka bayyana tana nufin wasu fitattun alamomin da ake iya shaida wani abu, su waɗannan alamomi su ke siffanta abin da ake so a yi magana a kansa. Don haka za a iya shaida adabin baka ne da kuma irin nagartarsa ta hanyar sifofin da ke biye. Waɗannan siffofi su ne ke tabbatar da nagartar kowane aikin adabi, Kuma su ke nuna irin hikima da fasahar da al`umma take da su. Ta hanyar waɗannan siffofi ake gane matsayin adabin baka da irin gudummuwar da ya bayar ga al`umma.

## 1.4 Jigo

A cikin Ƙamus na keɓaɓɓun kalmomin adabi, Shipley, (1955:417) ya bayyana ma'anar jigo da cewa: "Shi ne abin da ake magana a kai. Shi ne kuma abin da aka ƙudurta ko aka aikata. Ko kuma wani saƙon da wani labari ke isarwa."

Haka kuma in an duba {amus na Cuddon, (1977:680) An ce "Magana ta gaskiya, jigon wani rubutu ba yana nufin maganar da rubutun yake yi ba ne illa wata manufa ta musamman wadda aka bayyanata kai tsaye ko a fakaice."

Masana irin su Farfesa Yahaya, (1997:75) ya bayyana ma'anar jigo (waƙa) da cewa, jigo na nufin saƙo ko manufa ko bayani ko ruhin da waƙa ta ƙunsa wanda kuma shi ne abin da wa}ar ke son isarwa ga mai saurare, ko karatu, ko nazarinta. Ya kamata a lura a nan cewa wannan ma'ana za ta iya 'ɗaukar duk wani fanni na harshe, da adabi, da al'ada.

Farfesa Yahaya, I. Y. da sauransu, (1992:47) an bayyana ma'anar jigo da cewa, shi ne dai "saƙo" ko ginshi}in al'amari da abu yake ɗauke da shi. Wasu kuma kan fassara jigo da cewa shi ne "manufar abu" ko "ƙashin bayan abu" ko muhimmin darasin da yake ɗauke da shi ko yake koyarwa.

Gusau, (2003:28) Ya bayyana ma'anar Turke (jigo) da cewa, shi ne abin da (waƙa) take magana a kansa wanda ya ratsa ta tun daga farkonta har zuwa ƙarshenta. Wato dai turke shi ne ainihin manufar abu.

Mukhtar, (2004:31) ya ambaci jigo da cewa, shi ne ƙashin bayan labari, wato maƙasudin da aka gina labari a kansa.

Dangambo, (1981:5) ya ambaci cewa, abin da ake nufi da jigo shi ne saƙo, manufa, ko abin da (waƙa) ta ƙunsa, wato abin da take Magana a kai.

A takaice ma iya cewa jigo shi ne manufar da ake so a cimma a kowane irin abu. Masana da manazarta suna amfani da wannan kalma ta jigo don bayyana saƙo ko wata manufa ko kuma maƙasudin da ake so a isar ga al'umma. A wasan kwaikwayo, jigo na nufin manufa ko saƙon da aka gina wasan a kansa don mutane su himmatu ko su farka.

## 1.5 Salo

A waƙa, Abdullahi (2001:3) na cewa: salo na nufin duk wata dabara ko hanya a cikin waƙa wadda aka bi domin isar da saƙo. Ita wannan dabara ko hanya tana yi wa waƙa kwalliya ta yadda saƙon waƙar zai isa ga mai sauraro ko karatun waƙar. Ana ganin ba a yi kuskure ba idan aka ce wannan ma'ana ta salo da aka gani nan ita ce dahir a duk inda aka kaɗa ko aka raya, kuma ta kowace fuska aka dubi kalmar salo. Wannan ma'ana, ita ta sa masana irin su Dan'Gambo (1981) a cikin Abdullahi (2001:3) suka kawo wasu muhimman tubalan salo guda takwas. Waɗannan tubalan gina salo kuwa su ne:

1- Mallakar kalmomi
2- {irar Jumla
3- Nau'o' in jumla
4- Siffantawa
5- Rauji
6- Tsarin Tunani
7- Jaddadawa
8- Dangantakar tsari

Wannan shi ne ma'anar salo a waƙa. A ɓangaren zube kuwa, Mukhtar, (2004:34) na cewa; Abubuwan da akan nazarta a ƙarƙashin salo wanda kuma daga kansa ake yanke hukunci a ce salon marubuci ya ƙayatar, ya yi armashi, ko kuwa ragon salo ne da shi, sun haɗa har da nazarin irin kalmomin da ya yi amfani da su wajen gina labarinsa, da kuma adon Magana, da Karin Magana da maganganun hikima, da kuma tsarin ginin jimlolinsa. Salo na nufin duk wasu dabarun jawo hankali da marubuci kan bi wajen ƙoƙarin jawo hankalin mai saurаronsa, gani ko kuma mai karantawa. A nan ana nufin duk wasu dabarun jawo hankalin mutum zuwa ga abin da yake karantawa don a cinma fahimtar ainihin saƙon da ake son isarwa. Wannan ne ya haifar da wanzuwar salo iri daban-daban, waɗanda suka haɗa da miƙaƙƙen salo da salo mai armashi mai karsashi, da raggon salo. Haka kuma salo na iya zama sabo ko tsoho. Abin fahimta a nan shi ne, a zube idan aka ambaci salo, to ana duba harshen da marubucin littafin ne ya yi amfani da shi wajen isar da saƙonsa.
Amma a wasan kwaikwayo, Crow, (1983:55) ya ce: Salo ko harshe na nufin yadda harshen 'yan wasa ta dace da irin muƙamansu da aikace-aikacensu, wato salon da kowanne ɗan wasa ko 'yar wasa suka bi wajen

sarrafa harshensu a wasan kwaikwayo, wannan kam ya shafi dukkan fannonin wasan kwaikwayo. Idan an ce wane gwarzon wasa ne to akan gane shi ta abubuwan da yake faɗi ko ya aikata da kansa. Waɗannan abubuwa kuwa su ake son aga yadda aka zurfafa amfani da su don cimma manufar wasa. Ya zama wajibi (in har za a yi adalci a nazartar harshen 'yan wasa) a fahimci cewa ba ma'ana ta zahiri a zantuttukan 'yan wasa ita ce ka]ai za a duba ba har ma da sakamakon da maganar ta haifar a mahallin da aka yi ta. Wasan kwaikwayo harhaɗuwar wasu aikace-aikace ne don su isar da wata manufa, ashe faɗi-in-faɗin 'yan wasa dole ya kasance yana da dangantaka da aikace-aikacensu kafin a gane haƙiƙanin saƙon da ake son a isar.

Cuddons, (1955:655) na cewa; aiki ko wani motsi shi ma alamtawa ne (wanda ake amfani da shi a wasan kwaikwayo). Tauna leɓe na da wata manufa ta mugunta. Haka kuma tafa hannu na da manufar yabawa. ɗaga hannu kuwa na da manufar girmamawa ce. Duk waɗannan suna cikin abubauwan dubawa kafin a yi sharhi a kan hausar ɗan wasa ko 'yar wasa.

## 1.6 Zubi

Zubin wasa gagarumin fage ne na nazarin wasan kwaikwayo kowane iri ne, wanda yake buƙatar kulawa ta musamman. A cikin Abrams, (1981:159) an ce zubin wasan kwaikwayo na magana ne akan yadda aka tsara wasa ta yadda abubuwa suke gudana, daga wannan mataki zuwa wannan mataki. Wannan ya haɗa har da ayyukan 'yan wasa tun daga farko har zuwa ƙarshe domin cimma manufar shirya wasan.

Zubi na nufin yadda aka tsara abubuwa a cikin wasa, ko waƙa ko ƙirƙirarren labari. Aristotle, (1952:685) ya bayyana sifofin da zubin wasa ya ƙunsa kamar haka: "Ana buƙatar zubi ya kasance cikakke, wato ya kasance da farko da tsakiya da ƙarke. Kuma ya kasance yana da ɗinki wato haɗuwar aiki da wuri da lokaci inda idan aka gusa ko aka cire Ɗaya saura na iya rugujewa ko gurguncewa.

Wasa wanda ya amsa sunansa ko yake so ya amsa, dole ne ya kasance yana da haɗuwar waɗannan abubuwa guda uku, wato haɗuwar wuri da lokaci da kuma aiki. Idan ana so wasa ya ƙayatar a yi amfani da sananen wurare da ta}aitaccen lokaci kada a nuna cewa wasan ya ]auki wasu kwanaki ko shekaru ana gudanar da shi, ko da kuwa ana so a nuna irin wa]annan kwanaki ko shekarun a iya yin haka ta yin amfani da mai shela ko a sharar fage cikin rubutaccen wasan kwakwayo, amma a wasan kwakwayo na talbijin ana yin haka ne ta nuna cewa (bayan shekara kaza ko kwana kaza, ko makonni) sai kawai wasa ya ci gaba tare da jan hankalin mutane cewa sun yarda tamkar an yi wa]annan shekarun ko kwanakin.

Muhimmin abu na gaba a zubin wasa shi ne “Kauci”. Abrams, (1981:161) ya ce: Kauci na nufin a shigar da wani labari ko wata matsala ta daban mai dangantaka ko akasin haka da uwar labari ko wasa, akan yi haka ne don a ƙayatar da uwar sa}on da ake so a cimma.
Muhimmin abu na gaba shi ne waiwaye. Hausawa kan ce waiwaye adon tafiya. Abrams, (1981:161) Ya ci gaba da cewa: A tsari irin na wasan kwaikwayo akan yi waiwaye don ƙayatar da wasa ko jaddada wata manufa wadda ake son jama’a su rinƙa tuna ta a kowani lokaci a cikin ayyukan adabi.

Masana irin su Shipley (1955:310) Sun bayyana zubin wasan kwaikwayo na dauwama ne bisa sanannen tsari na farkon wasa a inda a wannan lokaci ake fara gina matsalar ko gabatar da ƙalu-balen da yake cikin wannan wasa, wanda zai sa mai kallo ya zaƙu da son ganin yadda za a warware wannan matsaralar ko ƙiƙi-ƙaƙa. Akwai tsakiyar wasa ko kuma in ce }ololuwar wasa, a nan ne matsalar wasan kan rinca~e. Wani lokaci rincabewar wasa na aukuwa ne a dai-dai lokacin da aka fara wasa. Wani lokaci kuwa a tsakiyar wasan ne ake samun wannan rinca~ewar. Sai ƙarshe ko kuma gangara inda ake samun lafawa da sulhu don warware matsalar cikin farin ciki ko kuma cikin ban tausayi.

## 1.7 Taƙaitawa (Summary)

Wannan darasi ya duba siffofin da ke bayyana nagartar adabin baka. An fahinci cewa baya ga nishaɗi, adabin baka yana taimakawa wajen ilmantarwa da faɗakarwa. Haka nan kuma nazartar salo da zubin kowane iri daga cikin nau`o`in adabin baka na bayar da dammar a fahinci irin gwanintar harshe da ƙyale-ƙyalen jawo hankalin da aka yi a cikin wannan adabin bakan.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

1. Nazarin jigo ko manufa abu ne mai muhimmanci ga adabin baka. Ɓarje guminka.
2. Bayyana abin da ka fahimta da salo da ire-irensa.

## 1.8 Manazarta Da Waɗansu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)


Abrams, M.H. (1981): *A Glossary of Literary Terms.* Six Edition Halt Rinehart &Wiston, New York.

Abdullahi, B.Y. (2001): *Salo Asirin Waka* Fisbas Media Kaduna.

Cuddons, J.A (1977). *A Dictionary of Literary Terms*. Reɓised Edition, London.

Dangambo, A. (1984). *Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga RayuwarHausawa*. Triumph, Kano

Gusau, S. M. (2003). *Jagoran Nazarin Wa}ar Baka.* Benchmark Publishers Limited, Kano.

Mukhtar, I. (2004). *Jagoran Nazarin {agaggun Labarai.* Benchmark PublishersLimited, Kano.

Shipley, J.T. (ed) (1955). *Dictionary of World Literary Terms.* Allens & UnwinLtd London.

Yahaya, I.Y. (da wasu) (1992). *Darussan Hausa Don Manyan MakarantunSakandare* 1 – 3, Ibadan Uniɓersity Press.

Yahaya, A. B. (1997). *Jigon Nazarin Wa}a* Fisbas Media Serɓice Kaduna.

## 1.9 Amsoshin Tambayoyi

1. Jigo da manufa na nufin saƙon da ake isarwa ga jama'a. Wanda zai iya kasancewa ta hanyar waƙa ko zube ko wasan kwaikwayo. Manufa da jigo ana ambatar su kai tsaye a wasu mahallan. Sai dai wani lokaci sai mai karatu ko mai sauraro ya ji ko ya karance rubutu gaba ɗaya, kafin ya ce ga jigon ko manufar labarin.
2. Salo dabaru ne na jan hankali da marubuci ko mai karatu ke yi domin jawo hankalin mai sararoko mai karatu. Yin amfani da kalmomin aron da adon harshe da gajerun jumloli a rubutu, duk za a iya ce musu salo.

## Kashi Na 2 Harshe

### Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ma’anar Harshe
 2.3.1 Harshe a Matsayin Kafa ta Sadarwa
 2.3.2 Harshe a Matsayin Kafa ta Bayyana Tunani
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amshoshin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa (Introduction)

Wannan darasi zai bayanin ma`anar harshe da kuma matsayinsa ga al`umma. Za a duba dangantakar da ke tsakanin harshe da al`umma musamman rawar da harshe yake takawa a matsayin kafa ta sadarwa. Haka kuma, irin gudummuwar da harshe ke bayarwa ga kaifafa tunani da faɗin ra`ayi da lallashi na daga cikin abubuwan da wannan darasi ya ƙunsa.

### 2.2 Manufar Darasi (Objectiƃes)

A ƙarshen wannan darasi, ana fatar ɗalibai su iya gane:

a. Ma`anar Harshe
b. Harshe a matsayin kafa ta sadarwa
c. Muhimmancin harshe ga adabin baka

### 2.3 Ma’anar Harshe

Masana irin su Yakasai, (2012) sun nua cewa a kullum cikin magana muke, muna magana da iyayenmu, da matanmu da mazajenmu, da ƙannenmu da yayyenmu. Haka kuma muna kuma magana da ‘ya’yanmu da maƙwabta da dai duk waɗanda cuɗanya ta haɗa mu da su. Wani lokaci ma mukan yi magana mu ka]ai. Mukan bayyana tunaninmu a fili idan muna farke, ko kuma mu riƙa yin magana cikin bacci idan muna mafarki. Haka kuma wani lokacin mukan riƙa rera waƙa don nishaɗi.

Baiwar da ɗan-Adam yake da ita ta amfani da harshe ita ce babban abin da ya bambanta shi da dukkan sauran halittu, har ya fifita shi bisa kansu. Kodayake dabbobi ma suna da tunani irin nasu, wanda kuma suke bayyanawa cikin hanyar sadarwa iri dabam-daban, amma babu wata dabba da take da hanyar sadarwa irin wadda ɗan-Adam yake amfani da ita, wato harshe.

A taƙaice, dangane da ma'ana, an bayyana Harshe da cewa, wata hanya ce ta bayyana kai da kuma hulɗa tsakanin mutane wadda dabbobi ba su da irinta (Sapir; 1956:1). Wannan ya zamo haka ne kuwa domin shi HARSHE, ya zama shi ne rai ko kuma zuciyar duk wani tunani da aiki na ɗan-Adam musamman dangane da abin da mutum ke ji game da kansa ko ƙasarsa, ko addininsa ko kuma yadda shi kansa ya ɗauki kansa (Lado; 1964:11). Wannan shi ya sa aka ɗauka cewa kalmomi ba wasu abubuwa ba ne illa tubalan ginin tunane-tunane da kuma ayyukan da 'yan-Adam ke tsarawa domin samun damar yadda za su iya fahimta, su kuma iya sarrafa mazaununsu (Lenneberg; 1967).

### 2.3.1 Harshe a Matsayin Kafa ta Sadarwa

Harshe muhimmiyar kafa ce ta sadarwa cikin zamantakewa. Wato idan aka yi amfani da harshe domin sadarwa, to ko shakka babu za a samu yana ɗamfare da al'ada ta hanyoyi daban-daban. Kalmomi da al'umma suke furtawa, da su ne ake bayyana al'amuran da suka shafi rayuwarsu, wato gaskiya da tunani da kuma harkoki da ake bayyanawa a matsayin tarin ilmi da sauran al'ummu ke fa'idantuwa da su. Hasali ma, kalmomi suna bayyana ɗabi'ar duk wanda ya yi amfani da su cikin tadodi. Ta wannan haujin, harshe yana bayyana hanyoyin rayuwa.

Bugu da ƙari, al'ummu ko rukunai na jama'a ba kawai suna bayyana ƙwarewa ba ne, wato suna kuma sarrafa ƙwarewa cikin harshe domin ɗorewar zamantakewa. Suna isar da saƙonni ta hanyoyi daban-daban kamar ta amfani da salula ko ƙib]au ko wasiƙa ko karatun jarida ko kuma hira da taɗi da juna kai tsaye. Hanyoyin da al'umma ke amfani da su (a magance ko a rubuce) suna da ma'ana wajen mu'amala musamman ma idan aka yi la'akari da yadda ake sarrafa hawa da sauka na muryar masu magana da karin lafazi da salon taɗi da kuma ishara. Ta wannan haujin, harshe yana ƙunshe da matakan sadarwa.

Haka kuma, harshe tsari ne na alamomi da ke ɗamfare da al'ada da ƙimar masu amfani da shi cikin amfani da harshe. Wato al'umma na kallon harshensu a matsayin alama ta tantance matsayi cikin zamantakewa. Ta wannan ƙaulin ma, harshe ya zama linzamin al'ada. Sauran maganar ita ce, harshe hanya ce ta bayyana da kuma musayar tunani da batutuwa da labarai domin yaɗa ilmi. Tare da dalilai na zamantakewa da tarihin canje-canje domin cigaba, ta wannan haujin, harshe yana matsayin wata kafar sadarwa ta musamman da take ɗamfare

ga ‘yan Adam, kuma wadda ta bambanta da sauran hanyoyin sadarwa kamar na dabbobi ko ƙirƙirarren harshe. Wato al’amari ne da ya ƙunshe rayuwar ɗan Adam gaba ɗayanta da kuma harshensa kamar Hausa.

### 2.3.2 Harshe a Matsayin Kafa ta Bayyana Tunani

Akan yi amfani da harshe don sosasa zuciyar mai sauraro. Maƙasudin wannan~angare na harshe shi ne ya daɗaɗa ko ya faranta, ko ya ~ata ko kuma ya tunzura zuciya. Yana da muhimmanci wajen yin raha da nuna tausayi da yin talla da kuma farfaganda (cusa ra’ayi). Da wannan harshe ne uwa kan lallashi ɗanta, saurayi yake latsa budurwa, kuma ɗan siyasa ke jan hankalin jama’a. Yakasai, (2012). Da harshe ne ake wanzar duk wani adabin baka da aka tsara. Shi ke taimakawa wajen furzar da tunanin fasihi har mutane su ji, su fahimci irin ƙyale-ƙyalen jawo hankalin da ke cikin wannan aiki na adabi. Saboda haka, harshe na bayyana irin tunanin da ke cikin zukatan mutane ko kuma irin tunaninsu game da rayuwa.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana ma’anar Harshe
**2.** Akwai dangantaka ta musamman tsakanin harshe da sadarwa? Bayyana yadda abin yake.

### 2.4 Taƙaitawa (Summary)

Muhimman abubuwan da wannan darasi ya koyar sun haɗa da bayyana ma`anar harshe a matsayin hanya ce ta bayyana kai da kuma hulɗa tsakanin mutane wadda dabbobi ba su da irinta. Haka nan kuma angano cewar harshe na taka muhimmiyar rawa wajen bayyan hulɗa tsakanin al`ummar da ke amfani da wannan harshe. Idan kuwa za ka ƙidaya muhimmancin harshe suna da yawa, amma a wannan fage, an fahinci adabin baka ba ya samuwa sai da taimakon harshen don wanzar da shi.

### 2.5 Manazarta Da Waɗansu Abubuwan Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

Lado, R. (1964): *Language Teaching* – A Scientific Approach, McGraw-Hill: New York.

Lenneberg, E. H. (1967): *Biological Foundations of Language*, Wiley, New York.

Yakasai, S A. (2012). *Jagorar ilimin Walwalar Harshe*, Sokoto. Garkuwa Media Serɓice Ltd.

## 2.6 Amsoshin Tambayoyi

1. Harshe kafa ce da sadarwa cikin zamantakewa. Hanya ce ta isar da saƙo da za ta iya kasancewa a rubuce ko a magance ko kuma ta hnayar ishara.
2. Sadarwa ba ta yiwu wa sai da harshe. Shi kuma harshe sinadari ne na isar da saƙo. Domin kuwa babu yadda za a ɗaya ya tafi ya bar ɗaya.

## Kashi Na 3 Wanzarwa

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Ma’anar Wanzarwa
3.3.1 Yadda Ake Wanzar da Adabin Baka
3.3.2 Gani Ya Kori Ji
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amshoshin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa (Introduction)

Wannan darasi ya taɓo wata siffa guda da ke bayyana adabin baka, kamar yadda aka yi bayani a darussan da suka gabaci wannan, adabin baka ko kuma adabin ‘ka’ adabi ne wanda ake ƙirƙirarsa da ‘ka’, a adana a ‘ka’ a kuma wanzar ta baka. Wannan wanzarwa kuma za mu iya kiransa da aiwatarwa. Wato ana iya aiwatar da adabin baka ko ta fannin magana ko kuma a aikace.

### 3.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Ana fata a ƙarshen wannan darasi, ɗalibai su ta gane yadda ake wanzar da adabin baka, wannan wanzarwa ta dogara ga irin nau`in adabin bakan ne. Misali idan waƙa ce ko kuma zube na baka, ana wanzar da su ta baka ba tare da motsin gaɓuɓɓan jiki ba. Idan kuwa wasanni ne masu siffar kwaikwayo, inda za a iya samun sauya kama ta murya ko ta shiga ko ta aikata wani aiki ko nuna yadda ake wani aikin, babu mamaki idan an sami kwaikwayo ko motsin jiki ko gwada yadda ake aiwatar da wani abu a ire-iren waɗannan misalai da aka bayar. Manufar dai a san cewa ana iya amfani da baka, haka nan kuma ana iya samun kwaikwayo a aikace.

### 3.3 Ma’anar Wanzarwa

Shaihin malami a nazarin adabi, Ɗangambo, (2008) ya bayyana yadda wanzar da adabin baka, wanzarwa na nufin yadda ake gudanar da adabin, wato yadda ake yin sa a aikace. Idan muka dubi yadda ake

gudanar da adabin baka a aikace, musamman waƙoƙi, a yanzu, za mu ga lallai akwai 'yan bambance-bambance da yadda ake yi a da, kafin zuwan Turawa. Misali, kamar yadda muka ambata can baya, makaɗan fada ba sa kaɗa wa kowa in ba jinin sarauta ba. Shi kansa Bature da ya zo ya yi mulkin mallaka, Sarkin Taushi ko Narambaɗa bai yi masa kiɗa ba, duk da ana ce masa "zaki". Amma yanzu mun ga wannan al'ada ta sauya, an karya ta. Kuma idan ka kwatanta ingancin waƙoƙin baka na da, kafin zuwan Turawa zuwa wajejen 1980, za ka ga babban bambanci, domin kuwa na da sun danne sun shanye na yanzu. Me ya sa? Dalili shi ne saboda yadda mawaƙan da ke tsayawa su shirya waƙa, su tsara ta, su tsaya a tsanake, cikin natsuwa da walwala su rera ta cikin lafazi da harshen da ya dace, tare da kiɗan da ya dace, su na yanzu ba sa yin haka. Sukan shirya waƙar cikin sauri da zaƙuwa da tunanin abin da za a ba su, kuma babu cikakkiyar biyayya tsakanin 'yan amshi da mai ba da waƙar. A sakamakon haka za mu ga tasiri da kwarjini da martaba da amfanin irin waɗannan waƙoƙi na baka kullum sai raguwa suke yi.

### 3.3.1 Yadda Ake Wanzar da Adabin Baka

Wanzar da adabin baka ya dogara ne ga nau`in adabin, idan waƙa ce galibi ana wanzar da ita ta baka ne tare da `yan amshi, da kiɗa, wani lokaci har da `yan rawa. Makaɗan ma sun bambanta kama tun daga ire-iren kayan kiɗan da waɗanda ake wa kiɗan. Idan kuwa zube ne na baka, misali tatsuniya ko ƙissa ko al`mara ko makamantar waɗannan, ana samu masu bayar da labari ne, wuri na musamman ake keɓewa da kuma masu saurare, zantukan hikima kuwa, ana aiwatar da su a kowane lokaci. Wasanni masu siffar kwaikwayo na buƙatar a yi su a aikace. Don haka, wajen wanzar da ire-iren waɗannan wasanni, misali wasannin tashe ko `yan kamanci ko wasannin gauta waɗanda ake wanzar da su lokaci-lokaci na shekara, suna buƙatar kayyaki na musamman yayin da ake gudanar da su.

### 3.3.2 Gani Ya Kori Ji

Da yawa daga cikin misalan adabin baka ganin su ake yi a lokacin da ake aiwatar da su, kaɗan daga ciki kuma sauraro ake yi da kunne, yayin da ake aiwatar da waɗannan ayyukan adabin, mutanen da ke kusa suna sauraron abin da ake faɗa. Idan kuwa wannan aiki na buƙatar sai an aiwatar da shi gaban `yan kallo, to fa a nan kuwa gani ya kori ji. Masana ilimin walwalar ɗan adam sun tabbatar da iƙrarin da ke cewa mutane sun fi saurin fahimtar abubuwan da suka gani da idanuwansu a bisa wanɗanda suka ji da kunne. Bari mu ɗauki misalin waƙar baka, ko zube na baka ko kuma ma aiki cikin kwaikwayo, duk waɗannan ana gabatar da su a gaban jam`a ne, kuma mutane suna ganin da idanuwansu ƙuru-ƙuru, ganin nan kuwa ko shakka babu ya kori ji.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

| | |
|---|---|
| 1. | Bayyana ma'anar aiwatarwa da yadda take bayyana ayyukan adabi. |
| 2. | Zaɓi biyu daga cikin nau`o`in adabin baka a bayyana yadda ake aiwatar da su. |

## 3.4 Taƙaitawa (Summary)

Wannan darasi ya yi tsokaci game da ma`anar wanzarwa. Kowane aikin adabi yana da tasa haryar da ake aiwatar da shi. Idan waƙar baka ce, ana wanzar da ita tare da amshi wani lokaci hard a kiƙa da r`yan rawa. Zube nab aka kuwa, yana bukatar mai bayar da labara da kuma masu saurare, haka nana wasannin kwaikwayon baka, shi ma yana bukatar masu wanzarwa a gaban `yan kallo.

## 3.5 Manazarta Da Waɗansu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Okpewho, I. (1990). *Oral Performance in Africa*. Ibadan Spectrum Books. Ltd.

…………. (1992). *African Oral Literature*. Bloomington IN Indiana Uniɓersity Press.

## Kashi Na 4: Saurare

### Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Ma’anar Saurare
 4.3.1 Dame Ake Saurare
 4.3.2 Ganewa
 4.3.3 Hoton Gurbin a Tunani
4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.7 Amshoshin Auna Fahimta

### 4.1 Gabatarwa (Introduction)

A wannan kaso za a yi bayani ne dangane da abin ake nufi da saurare a matsayin wata siffa ta adabin baka. Don haka, za a bayyana ma'anar saurare da sanin abin da ake sauraren da shi da yadda ake iya gane abin da aka saurara da kuma yadda ake samun gurbin tunani a sakamakon abin da aka saurara.

### 4.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufa a nan ita ce, koyar da babban siffar adabin baka wato saurare wanda a ƙarshen darasin ake so almajirai su fahimci:

- Ma'anar saurare
- Abin da ake saurare da shi
- Abin da ake nufi da ganewa
- Yadda hoto yake a gurbin tunani

### 4.3 Ma’anar Saurare

Idan aka ce saurare to ana nufin ' yin shiru ko tsit don a ji magana' ko kuma ' yin tsumayi ko dakace ko jiran wani mutum ko wani abu'. Sannan akwai kalmar 'saurara' wadda aka bayyana ma'anarta da 'kasa kunne da niyyar jin sauti' ko kuma 'Tsumayi ko dakata ko jira'. Ƙamusun Hausa (2006:394). To a wannan ɓarayi ana magana ne a kan saurare irin na magana wanda ya danganci adabin bakan Bahaushe.

### 4.3.1 Dame Ake Saurare

Tun daga bayyana ma'anar saurare za a iya fahimtar cewa ana saurare ne da kunne wanda ƙamusun Hausa (2006:254) ya ce kunne shi ne: "Sashen jiki da ke saman kunci wanda ake jin sauti." Shi kuma sauti na iya kasancewa na magana ko wani abu daban, kamar ƙarar kiɗa ko faɗuwar wani abu ko motsa wani abu da sauransu ba iyaka.

### 4.3.2 Ganewa

Ganewa dai na nufin 'fahimta' ko 'sani' wanda kan faru a yayin da kunne ya saurari wani abu, take sai ya aika wa ƙwaƙwalwa wadda ita ke da alhakin ɗaukar nau'in saƙon da ya iske ta. Daga nan wani sashen ƙwaƙwalwa zai ɗauki aikinsa na sarrafa wannan saƙo har a samu fahimtar wannan sauti. Gane batun da aka ji zai iya ɗaukar fuskoki daban-daban. Misali:

Mai saurare zai iya ƙoƙarin fahimtar ko wane irin ƙara ko sauti kunnensa ya ji. Shin sautin magana ne ko kukan wata dabba ko wani abu daban. Idan sautin magana ne, zai iya fahimtar wannan muryar namiji ne ko mace, babba ko yaro da sauransu. Sannan sautin maganar nan ihu ne ko kuka ko magana sosai ko waƙa ce ko tasuniya? Idan kuma sauti ne irin na dabba, to wanda ya ji zai fahimci kukan wace dabba ce kunnensa ya ji.

Haka kuma, mai saurare na ƙoƙarin fahimtar saƙon sautin da kunnensa ya ji ba tare da ya yi dogon tunani ba. Misali, yayin da mutum ya ji an ce: "Ga ta nan ga ta nanku" zai yi saurin gane cewa tatsuniya za a gabatar. Ko kuma ya ji ƙarar buga tambari zai fahimci sarki ya fito Fada. Har wa yau, yanayin sauti ko maganar da mai saurare ya ji da kunnensa na iya haifar masa da fahimtar da lallai dole sai ya nemi fassara ko ƙarin bayani. Misali idan mai saurare ya ji wasu fasahar baka, kamar karin magana ko habaici cikin zance, mafi yawanci sai ya buƙaci fassara ko ƙarin bayani.

Akwai kuma abin da kunne in ya ji, zai haifar da fahimta mai tasirantar zuciya. Misali, idan mai sauraro ya ji kuka ko dariya, dole ya ji ɗarsashin baƙin ciki ko zullumi ko tausayi ko farin ciki a zuciyarsa domin ya gane abin da sautin ke nufi.

### 4.3.3 Hoton Gurbin a Tunani

Hoton gurbin tunani na faruwa ne a yayin da aka saurari wata ƙara ko sauti, sai ƙwaƙwalwar mai sauraron ta sarrafa ganin wannan siffar abin da aka ji. Misali, idan aka ji ƙarar mutsuttsuka takarda, kila kuɗi ake ƙirgawa ko kuma wata takardar karatu ake motsawa. Idan ƙirgar kuɗi ne,

maganar da za a yi za ta dace da wannan aiki. A irin wannan yanayi, mai sauraro sai ya riƙa ganin kuɗin kamar da gaske yake kallo. Tamkar a waƙar baka, inda mawaƙi kan siffanta wani abu dangane da kyau ko muninsa ko girmansa ko ƙarfinsa da sauransu, dole ne mai saurare tunaninsa yay i saurin sarrafuwa har ya ga hoton abin da ya ji ana siffantawa. Ko ma ba siffantawa aka yi kai tsaye ba, akwai maganar da za ta iya tilasta wa mai saurare ganin hoton abin da aka ambata. Misali, a cikin waƙar baka Barmani Coge da ta ce:

Kuma an je wurin barka
Ga uwargida bisa wundi
Ɗayar a kan `yar kanti,
Da wadda ba ta sana'a
Ta ɗauki guntun keso
Ta kakkaɓe shi ta zauna.
(Rabi 2011)

Duk kunnen da ya ji wannan, to babu shakka sai tunaninsa ya ɗauka ya sarrafu ta yadda zai ga hoton mata uku waɗanda suka je barkar haihuwa, kuma kowacce da irin shigarta da irin nau'in tabarmar da suka zauna a kai. Haka lamarin ke kasancewa a tatsuniya, domin tana ƙunshe da maganganu masu tilasta tunanin mai sauraro a tafarkin ganin hoton abin da ake magana a kai.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

| |
|---|
| 1. Bayyana ma'anar saurare da matsayinsa a adabin baka.<br>2. Da me ake saurare? Yi bayani tare da misalai |

## 4.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kaso an kawo ma'anar saurare da abin da ake sauraren da shi. An kuma yi bayani kan yadda ake fahimtar abin da aka saurara tare da yadda ake samun sarrafuwar tunanin da mai saurare ke ganin hoton abin da ya ji da kunnensa.

## 4.5 Manazarta DaWaɗansu Abubuwan Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Rabi, M. (2011): "Ɗabi'un Mata a Bakin Mawaƙan Baka na Hausa" Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsuna da Al'adun Afrika, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

## 4.6 Amsoshin Tambayoyi

**1.** surare shi ne mutum ya saurari ko jira aukuwar wani abu ko wani al’amari. Zai iya kasancewa a yi shiru domin jin wata Magana daga bakin mai magana. Wani lokaci ana sauraron Magana ne ko sauti da kuma fahimtar abin da aka faɗa.

2. a Ana saurare da kunne

b Ana saurare da na’ura
c Ana saurare da sassan jiki

## Rukuni Na 3 Matsalolin Tattara Adabin Baka

Kashi Na 1 Matsalar Rashin Rubutu/Adana
Kashi Na 2 Matsalar Shekaru
Kashi Na 3 Al'ada
Kashi Na 4 Ragi ko Ƙari

## Kashi Na 1 Matsalar Rubutu

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma'anar Rubutu
  1.3.1 Abubuwan da ake Rubutu a kai (Ganye Dutse, Fatu, Duma, Takarda)
  1.3.2 Matsalar Tawada
  1.3.3 Adana
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amshoshin Auna Fahimta

### 1.1. Gabatarwa (Introduction)

Matsalar iya rubutu ko sifanta tunani a rubuce ita ce babbar matsalar da aka danganta ta da adabin baka wadda wannan kashi zai tattauna a kai. Duk hikimomin da fasahar baka waɗanda baƙar fata suka samar ba a ɗauke a matsayin adabi ba saboda matsalar ba a rubuta su ba. Don haka za a bayyana ma'anar rubutu da abubuwan da ake amfani da su wajen yin rubutu da matsalar da ke tattare da su.

### 1.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce, ana so almajirai su fahimci cewa adabin bakan Bahaushe na da babbar matsala ta rubutu tun farkonsa har ya zuwa yau. Shi ya sa ake so almajirai su san waɗannan:

- Ma'anar rubutu
- Abubuwan da ake rubutu a kai
- Matsalar tawada
- Adana

## 1.3 Ma'anar Rubutu

Ƙamusun Hausa (2006:374) ya bayyana ma'anar kalmar 'rubutu' da cewa shi ne: "Zanen magana a kan takarda ko allo ko a wani bigire."

Haka kuma, Malumfashi (2019:1), ya bayyana ma'anar rubutu da cewa: "Wata kafa ce ta mayar da tunani ko harshe a cikin takarda." Sai dai cikin bayanansa, an fahimci cewa rubutu ba lallai sai a kan takarda ba domin wannan sanance ne na baya-baya tunda an tabbatar da cewa rubutu fasaha ce ta kowace al'umma a doron ƙasa. Sai dai kowace al'umma da abin/abubuwan da take amfani da shi/su wajen yin rubutu saɓanin takarda.

### 1.3.1 Abubuwan da ake Rubutu a kai (Ganye Dutse, Fatu, Duma, Takarda)

Rubutu ya kasance ana yin sa a kan abubuwa da dama in an ɗebe sanannen abun da aka fi sani a yau, wato 'takarda'. Malumfashi, (2019:1) ya bayyana cewa: "Kowace al'umma a doron ƙasa da irin nata yanayin rubutun, ba dole sai a takarda ba; wasu na yin sa a jikin kogo ko itace ko ganyaye ko fatu ko duwatsu. Wasu al'ummomi kuma ta alamci ko nuni ko sassaƙe-sassaƙe ko makamantan haka da ake ganin ajiyayyen tunaninsu ko harshensu, wasu kuma ta hanyar kiɗa ko waƙa ko hito ko wani dabashiri da suka tanada domin tallafar nasu tunanin ko harshen."

Hausawa suna daga cikin al'ummomin da suka yi rubutu a kan wasu abubuwa kafin zuwan takarda a gare su. Abubuwan da suka yi wani rubutu a kai akwai duma, da fatun dabbobi da kuma tsaga a jikin fatar mutum wadda ake kira tsagar gargajiya da kuma a kan allo wanda ake sassaƙa shi daga itace. Duka alamomi ne waɗanda ke bayyana wani tunani na al'umma a wancan zamani dangane da bambance-bambancen garuruwa da abin da ya shafi sana'o'i da sauransu.

### 1.3.2 Matsalar Tawada

Kalmar tawada tana da ma'anoni kamar uku a Ƙamusun Hausa (2006:434), amma wadda ake nufi a nan ita ce wadda aka ce: "Baƙin ruwa mai kauri wanda ake tsoma alƙalami ana rubutu da shi."

\Bisa fahimta, ita tawada tana nufin ruwan rubutu wanda akan tanada musamman daga wasu nau'o'in itace kamar ɗinya, a haɗa da wasu sinadarai kamar ƙaro a dafa har a samar da ita galibi baƙa ƙirin a launinta, amma akwai ta icen ɗinya da launinta ke kama da ruwan zuma mai duhu.

Idan an fahimci ko mece ce tawada, to sai a komo ga bayanin matsalarta a fagen adabin bakan Bahaushe. Kamar yadda aka sani, amfani da tawada a yi rubutu daga baya ya shigo wa rayuwar Hausawa, yayin da su kuma sun daɗe suna wanzar da adabinsu da baka ne. Idan sun wanzar da adabin nasu kuma suna adanawa ne a 'ka' ba a rubuce ba. ko a lokacin da addini ya samu ƙarfi a ƙasar Hausa, an yi amfani da tawada ne mafi akasari wajen koyar da addinin Musulunci. Ko da aka samu waƙoƙi ma, babu na baka da aka rubuta, balle a samu sauran fannonin adabin baka irin su tatsuniya da azancin maganganu da sauransu.

### 1.3.3 Adana

A Ƙamusun Hausa (2006:2) an bayyana ma'anar 'adana' da cewa shi ne: "Ajiye abu yadda ba zai salwanta ko ya lalace ba."

Dangane da adabin bakan Bahaushe adana matsala ce tun asali da ta sa ɗimbin ayyukan adabin Bahaushe suka salwanta. Kamar yadda aka sani, ana adana adabin baka ne tun farko a 'ka'. Daga baya zamani ya kawo sauyi inda ake iya adana adabin baka a rubuce ko a cikin fayafayen sidi da kaset-kaset da sauran hanyoyi irin na zamani. Duk da haka, in an ga adabin baka ya adanu to ta fuskar nazarce-nazarce ne ko kuma a samu a gidajen rediyo. Su ma ɗin akwai sakaci sosai na rashin tattala kayayyakin da ke ɗauke da adabin bakan yadda ya kamata.

### Auna Fahimta

1. Me ka fahimta da ma`anar rubutu, kuma ta ina rashin iya rubutu ya da kushe adabin baka?
2. Rattabo hanyoyin adana tunani a rubuce na gargajiya, sa`annan a daddagi biyu daga daga ciki.

## 1.4 Taƙaitawa (Summary)

Wannan darasi ya duba matsalolin da ke tattare da samar da adabin baka, an gwada cewa Turawa sun ƙyamaci hikimomi da fahahar baka ta al`ummar afirka ba don komi ba sai don ba a rubuce suke ba. Matsalar farko da wannan darisi ya duba ita ce ta rashin rubutu. Ba za a kira mutumin da bai iya rubutu da karatu jahili ba, domin ilimi a ƙwaƙwalwa yake kuma hanyar wanzarwa tana iya kasancewa ta baka ko ta rubutu. Haka nan kuma, darasin ya duba ire-iren abubuwan da ake yin rubutu a kansu waɗanda mutanen da suka yi amfani da su. Daga nan, an duba matsalar rashin tawada da ta adana a matsayin matsalolin da ke tattare da adabin baka.

## 1.5 Manazarta Da Wasu Abubuwa Na Nazari (Referenc/Further Reading)

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello Uniƃersity Press.

Malumfashi, I. (2019): “Kunnenka Nawa? Labarin Hausa a Rubuce” a Cikin

*Labarin Hausa a Rubuce 1927-2018* ISSBN: 978:978-55352-8-0. Zariya: Ɗab’in Maɗaba’ar Jami’ar Ahmadu Bello

## 1.6 Amsa Tambayoyi

**1.** Rubutu hanya ce ta rubuta ko bayyana tunani ɗan adam a kan littafi. Rubutu alamomin da ake zayyana su bisa littafi, su kuma bayar da ma’ana. Rubutu alama ce da ke bayyana ko fito da ci gaba da kuma fasahar al’umma a duk wurin da suke.

2. hanyoyi Adana tunani na adabi sun haɗa da:

a.kaset-kaset
b rediyo
c talabijin
d garmaho
e salula
f da sauran kayan shirin game duniya.

## Kashi Na 2 Ma'anar Tsufa/Shekaru

### Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ma'anar Tsufa
  2.3.1 Yadda Tsufa Take Tasiri ga Bayani
  2.3.2 Gushewar Riƙe Abu
  2.3.3 Kwan Gaba-Kwan Baya
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amshoshin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa (Introdauction)

Tsufa ko shekaru ɗaya ne daga cikin batutuwan da suke kawo tarnaƙi ga adana adabin baka. Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan ma'anar tsufa da yadda tsufa ke tasiri ga bayani har ta haifar da gushewar riƙe abu da kuma kwan-gaba-kwan-baya.

### 2.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce koyar da yadda tsufa ke kawo tarnaƙi ga adana adabin baka. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma'anar tsufa
- Yadda Tsufa ke tasiri ga bayani
- Bayyana tsufa ke haifar da gushewar gane abu da kwan-gaba-kwan-baya

### 2.3 Ma'anar Tsufa

Tsufa na nufin kaiwa munzalin tsoho, wato a tsofe ko a daɗe a duniya, (CNHN, 2006 : 459). Kenan, tsawon lokacin da mutum ya kai a raye ko daɗewarsa a doron ƙasa shi ke haifar da tsufa gare shi. Wanda ya daɗe a duniya kuma shi ne tsoho, mace kuma tsohuwa, jam'i tsofaffi. Shekarun tsufa suna farawa ne daga shekara sittin zuwa sama. Masu adadin waɗannan shekaru sukan kasance masu rauni saboda jikinsu ya yi sanyi,

shekarun sun ja, tunaninsu ya raunata. Domin haka riƙe abu yana yi masu wahala.

### 2.3.1 Yadda Tsufa Take Tasiri ga Bayani

Duk bayanin da ba a rubuce yake ba, wato yana 'ka' ne, an haddace shi a ƙwalƙwalwa, yakan iya fuskantar tasgaro lokacin da tsufa ya zo, domin ƙwaƙwalwar da ta riƙe bayanin ta yi rauni sakamakon tsawon lokaci. Shi ya sa idan aka iske tsoho ko tsohuwa domin neman wani bayani game da wani nau'in adabin baka, za a iske akwai giɓi a wasu bayanan sakamakon tsufa ta sanya ba komai ƙwaƙwalwar za ta iya riƙewa ba, in ma ta riƙe ɗin a da, to tsufa ya sanya bayanin ya sami tasgaro.

### 2.3.2 Gushewar Riƙe Abu

Har ila yau, tsufa kan haifar da gushewar riƙe abu ta yadda abin da ƙwaƙwalwa ta haddace tsawon lokaci za a iya mantawa da shi saboda halin jiki da jini. Mantuwa siffa ce daga cikin siffofin tsufa kuma ɗabi'a ce da ake samun galibi tsofaffi da ita. Shi ya sa za a iya tattaunawa da tsoho ko tsohuwa yanzun nan, in an jima kaɗan ya manta, ko an tayar masa da batun za a sha fama kafin ya tuna. Irin wannan ɗabi'a tana shafar adabin baka, shi ya sa abin da aka riƙe a *ka*, game da adabi, zai iya gushewa lokacin da tsufa ta zo.

### 2.3.3 Kwan Gaba-Kwan Baya

A wani yanayin, tsufa kan haifar da kwan-gaba-kwan-baya wajen bayani kan adabin da ke riƙe a ƙwaƙwalwa. Saboda yanayi na tsufa da shekaru masu yawa a doron ƙasa da ke haifar da raunin ƙwaƙwalwa, akan sami harɗewar bayani a kan aikin adabi, wato yayin da ake bayani a kan wani abu na adabi, sai an yi nisa sai a dawo farko, can kuma a tsallaka wani ɓangaren, in an ɗinke nan a ɓalle nan, haka dai a yi ta kwan-gaba-kwan-baya. Wannan duk tsufa ce take haifar da hakan.

**Auna Fahimta**

| | |
|---|---|
| 1. | Bayyana ma'anar tsufa |
| 2 | Tattauna yadda tsufa ke tasiri ga bayani ta fuskar adabin baka |

## 2.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi an tattauna a kan matasalar tsufa ko shekaru ta fuskar adana adabin baka. Kashin ya ƙunshi bayanai kan ma'anar tsufa da yadda tsufar ke zama tarnaƙi ga adana adabin baka.

## 2.5 Manazarta Da Wasu Abubuwa Na Ƙara Darasi (Referenc/Further Reading)

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

## 2.6 Amsoshin Tambayoyi

**1.** Tsufa na nufin mutum ya kai wasu shekaru ko daɗewa a duniya. Idan mutum ya jima a duniya shi ake ce masa tsoho.

a. Kwan gaba kwan baya. Tsufa na sa ƙwaƙwalwa yin ƙwan gaba ƙwan baya a karatu ko rubutun adabi. Wanda yin hakan, matsala ce babba a duniyar adabi.

b. Rashin riƙe abu. Ma'ana ƙwaƙwalwa ba ta iya riƙe wasu abubuwa mihimmai na adabi. Wasu lokuta ma idan shekarun suka ja, sai ƙwaƙwalwar ta zama me mantuwa karkaf.

## Kashi Na 3 Al’ada

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Ma’anar Tsufa
 3.3.1 Yadda Tsufa Take Tasiri ga Bayani
 3.3.2 Gushewar Riƙe Abu
 3.3.3 Kwan Gaba-Kwan Baya
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amshoshin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa (Introduction)

Wannan darasi zai yi duba ne kan ma`anar al`ada da kuma yadda al`adar Bahaushe kan iya zama cikas wajen samar da watsuwar nau`in adabi bai ɗaya. Za a duba bayanan da masana suka yi kan al`ada, an kuma tsaya ga fannoni guda uku muhimmai na al`ada, wato Aure da haihuwa da mutuwa. A cikin an ɗan zaƙulo wuraren da ake jin za su iya haifar da cikas wajen tattara ayyukan adabin baka na Bahaushe.

### 3.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

A ƙarshen wannan darasi, ana fata ɗalibai su iya gane ko me ake nufi da al`ada da kuma muhimman ɓangarorin al`ada. Wajen gudanar da waɗannan al`adu ne ake samun shigar gizai gizai na adabin baka. Misali a cikin al`adar aure ake samun kaɗe-kaɗe da waƙe-waƙe na samari da `yan mata. Don haka ta yaya al`ada za ta iya zama cikas wajen tattara ayyukan adabin baka? Gano waɗannan amsoshin su ne manufofin wannan darasin.

### 3.3 Ma’anar Al’ada

Ainahin wannan kalma ba bahaushiya ba ce, aro ta Hausawa suka yi daga Larabci. Sai dai kuma, ganin cewa are-aren kalmomi tsakanin Hausa da Larabci da]a]]en al’amari ne a tarihi (Ibrahim, 1982) ya sa ba za mu bi diddigin tarihin ba. Duk da haka, a luggar Larabci, al’ada na nufin wani abin da aka saba yi ko ya saba wakana ko aka riga aka san da

shi. Da wannan dalili ne wasu masana furu'a ke gabatar da wani zancen hikima mai cewa "*Al'adatul baladi kas sunnah*" wato al'adar da gari ya saba da ita kamar sunnah ce (Bunza,2006).

A harshen Hausa kuwa, masana sun kalli al'ada da ma'anoni mabambanta. Bunza (2006) cewa ya yi 'Al'ada tana nufin dukkanin rayuwar ɗan Adam tun daga haihuwarsa zuwa kabarinsa'. Wato a ko'ina mutum ya samu kansa, duk wata ɗabi'a da ya tashi da ita tun farkon rayuwa ya tarar a wurin da ya rayu, ko yake rayuwa, ita ce al'adar da za ayi musu hukunci da ita. Saboda haka, babu wata al'umma da za ta rayu a doron ƙasa face tana da al'dar da take bi, kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata al'ummar daban.

Shi kuwa Taylor (1871) ya bayyana ma'anar al'ada da cewa 'Al'ada ta ƙunshi dukkan abubuwan da al'umma ke yi waɗanda suka haɗa da ilmi da imani da fasaha da ƙere-ƙere da tarbiyya da horo da hani da sauran wasu halaye da ]an-Adam ke yi a matsayinsa na ]an-Adam'. Sai kuma Gidden (1989) mai ganin 'Al'ada a matsayin ɗabi'o'in kirki wa]anda al'umma ta aminta da su da horo da hani da nishaɗantarwa da irin ƙere-ƙeren da al'umma ke yi da hannunta.

Ma'anar al'ada ga masana al'ada ba ta wuce "Wata tsararriyar kimiyyar rayuwar mutane tun daga haihuwarsu har zuwa kabarinsu ba, falsafar al'ada da kimiyyarta ya ƙunshi fasahar mutane da aƙidojinsu da taskar ayyukan da suke sarrafawa da hannayensu da bakunansu, da gaɓɓansu da abubuwan da suka yi imani da su. Waɗannan abubuwan an gaje su ne, ko ƙirƙiro su aka yi, ko an garwaya su da wasu baƙin al'adu, duk suna cikin hurumin nazarin al'ada". Bunza, (2011:2).

Al`ada ita ce abubuwan da mutum ya saba yi, yau da gobe. Akwai al`adu da dama waɗanda Hausawa ke yi waɗanda suka shafi aure, da haihuwa da mutuwa. A ciki za iya samun wasu abubuwa waɗanda ka iya zama matsala wajen tattara adabin baka. Misali idan ana buƙatar bayanin ire-iren waƙen da mata ke yi ko surkullen da suke yi wajen haihuwa, ba dole ne ne a sami cikakken bayanin abin da ake so ba. Al`adar wani garin kuma ta bambanta da ta wani garin, duk da yake akwai inda suka yi tarayya, amma bambancin al`ada kan shafi ingancin ko wanzar da adabin baka bai ɗaya.

### 3.3.1 Yadda Al'adar Wuri Take

Ko shakka babu yadda al`adar wuri take ta bambanta da wasu al`adun wasu mutanen. A nana ana son a fahince cewa idan ana maganar adabin baka na baƙar fata, za a iya samun bambance-bambance nmasu taroin yawa a al`adun mutanen Afirka. Ga mutanen wani yanki na Afirka ta kudu, idan an yi baƙo kuma ana son a yi masa tarba da maraba, akan

haɗa hannaye biyu ne a mare shin a lokaci guda. Wasu kuwa sun yin gwalo ne da nufin maraba ga baƙo abin ƙauna. Waɗannan al`adu guda biyu da aka yi maganarsu a sama, idan Bahaushe ne ka yi masa waɗannan abubuwa, to da wuya ku kwashe lafiya. Ba don komi ba sai don shi a al`adarsa cin fuska ne da kuma wulaƙanci. Saboda haka yadda al`adun wani wuri suke sun bambanta da yadda ta wani wuri suke.

### 3.3.2 Tarihin Al'adu

Tarihin al`adu na tafiya kafaɗa da kafaɗa da yadda al`umma take gudanar da rayuwarta. Da farko dai ga wasu masanan, sanadiyyar yawace yawace ne ɗan Adam ya fahinci yin farauta da kashe namomin daji domin ya sami abinci. Ta hanyar jefar da fatun dabbar da aka feɗe ne ake hasashen an sami ganga wadda aka fara kiɗa da ita. Haka nan kuma, ana jin ta hanyar kwarzanta jarumai ne udan sun dawo yaƙi aka sami adabin baka irin su kirari da take da dai sauran makamantan waɗannan. Kusan babu wani haƙiƙanin lokaci na wata al`umma da za a ce gashi a wannan lokaci ne aka fara adabin baka. Don haka, ya kamata mai tattara adabin baka ya san tsarin al`adun al`ummar da yake tattara adabinta. Rashin sanin tsarin al`adar kan iya shafar tattara adabin wannan al`ummar.

**Auna Fahimta**

1. Me ake nufi da al`ada?
2. Kamar yadda mazauna wuri suka bamabanta haka ma al`adarsu ta bambanta. Ka an yarda?

### 3.4 Taƙaitawa (Summary)

Wannan darasi ya bayyanawa mai karatu ma`anar al`ada kamar yadda yadda masana suka ambata. A fahinci al`ada bat a wuce tsarin rayuwa da al`umma suka yarda da shi wanda ya kasance karɓaɓɓe ga al`ummar ta kowanne ɓangaren rayuwa. Al`ada na nufin abubuwan da aka saba yi kullum kuma mutane suka yarda da su, idan ma wani ya aikata akasin haka ana masa kallon ya yi wani abin da ba dai dai ba.

## 3.5 Manazart Da Wasu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)


Bunza, A. M. (2002) "Nazarin Al'adun Da Ke Cikin Kaset-Kaset Na Hausa Da

Littafan Zamani (1980 – 2002)". Maƙalar Da Aka Gabatar A Taron Ƙarawa Juna Sani Jami'ar Usman Ɗanfodiyo Sakkwato.

……………. (2006) *Gadon Feɗe Al'ada.* Tiwal Nigeria Limited, 16th Akinbaruwa Street, Off Atunrase Street, Surulere, Lagos.

……………….. (2011) "Al'adun Hausawa Jiya da Yau: Ci Gaba ko Lalacewa?"

Takardar da Aka Gabatar a Taron Bukukuwan Ɗalibai na Makon Hausa. Sashen

Nazarin Harsuna Nijeriya da Ilimin Harshe, Jami'ar Jihar Kaduna, Kaduna.

Khalil, I. (2009) Cakuɗe cakuɗe Biyu Jami'ar Usman Ɗanfodiyo Sakkwato.n Al'adu a fina-finan Hausa. Kundin Digirin Na

Liman, A. A. (2008) "Hegemony and Mass Mediated Culture: A Study of Popular Culture Trends in Postcolonial Northern Nigeria" Ph. D Thesis. Department ofEnglish, Faculty of Arts, Ahmadu Bello Uniɓersity Zaria.

Taylor, E. (1871). *The Science of Culture*. Cambridge Uniɓersity Press.

## 3.6 Amsoshin Tambyoyi

1. Al’ada na nufin abubuwan da mutum ke yi ya kuma saba yi tun daga haihuwarsa har zuwa kabarinsa. Al’ada a taƙaicce duk abin da mutum ya saba yi ko wasu al’ummu suka saba, ita ce al’adear wannan mutumin ko kuma waɗannan mutanan.
2. Kazalika duk wurin da aka samu mutane na rayuwa, to suna da al’adarsu a wurin. Hka zalika a sauran wurare ma, duk abin da aka iske a wurin da wannan mutanen key i su ma it ace al’adarsu. Saboda haka, dukkan mahallai na da irin al’adunsu waɗanda suka bambanta da juna.

# Kashi Na 4 Matsalar Ragi ko Ƙari

## Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Ma'anar Ragi
 4.3.1 Ragin Yanayi
 4.3.2 Ragi na Ma'ana
4.4 Ma'anar Ƙari
 4.4.1 Ƙari na Yanayi
 4.4.2 Ƙari na Ma'ana
4.5 Taƙaitawa
4.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.7 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.8 Amsoshin Auna Fahimta



## 4.1 Gabatarwa (Introduction)

Kamar yadda mutane suka bambanta, haka ma al`adunsu suka bambanta, ko a ƙasa ɗaya, ana iya samun bambancin al`adu. Wannan bambanci zai iya haifar da bambanci ga tsarin tunani da yadda mutane ke fuskanta abubuwan rayuwa. A ƙasar Nijeriya akwai mutane masu harsuna mabambanta, fitattu daga cikinsu, sun haɗa da Yarbawa da Ibo da kuma Hausawa, ashe don an sami bambanci tsakanin waɗannan al`ummomi duk da kasancewarsu a ƙasa guda ba abin mamaki ba ne. Idan ma muka dawo ga al`ummar Hausawa, ana samun bambanci tsakanin Sakwatawa da Zage-zagi da Katsinawa zuwa Kanawa ko Daurawa. Saboda haka wannan bambanci wuri na iya shafar adabin bakan da ake samu. In an tashi bayar da bayanin wani nau`in adabin baka misali tatsuniya a wani gari, za a iya samun ragi ko ƙari na wannan tatsuniya a wasu wuraren. Wannan darasi zai duba yadda ragi ko ƙari ke shafar wanzar da adabin baka da kuma irin abubuwan da kansa ba a samun adabi bai ɗaya.



## 4.2 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da yadda ragi ko ƙari ke kawo tarnaƙi ga wanzar da adabin baka. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma’anar ragi da ƙari
- Yadda ragi ko ƙari ke tasiri ga wanzar da adabin baka
- Bayyana ire-iren ragi da ƙari wanda ke shafar adabin baka.

## 4.3 Ma’anar Ragi

Ƙamusun Bayero na Kano (2006:363) Ya bayyana ragi a matsayin ɗebe kaɗan daga cikin wani abu mai yawa. Wato rage yawan wani abu ko sauƙaƙa nauyin wani abu. Haka nan kuma an bayyana ragi a matsayin ɗebe wani abu a cikin farashin asali. Wannan na nuni da cewa ragi shi ne rashin samun cikar wani abu na yadda yake tun farko. Idan ana magana kan adabin baka, duk wani nau`in adabin baka wanda wajen wanzar da shi aka sami ɗebe wani abu ko wani yanki na daga asalin siffarsa da aka sani tun farko shi ake nufi da ragi. Wannan ragi kamar yadda za mu gani nan gaba, na iya shafar siffa ce ko yanayi ko manufa.

### 4.3.2 Ragin Yanayi

Yanayi a nan, na nufin hali ko siffar da wani abu yake ciki. Idan an daganta da yanayi irin wanda ɗan Adam yake rayuwa, za a iya cewa muna da yanayi na damina da rani da sanyi ko zafi da dai sauransu. Manufa a nan ita ce, a fahinci cewa yanayi na nufin halin da abu yake ciki, idan mun danganta da adabin baka don gwada yadda ragin yanayi ke zama a matsayin wata matsala ta musamman, to ana nufin rage yadda siffar adabin baka yake. Bari mu ɗauki tatsuniya a matsayin misali, idan muka ɗauki tastuniyar `yar Bora da `yar Mowa, inda aka nuna dukansu sun fita biɗar neman Ruwan Bagaja, a wannan tatsuniyar akwai kuguna na abinci da yawa da aka lissafa waɗanda sai an ƙetara su kafin a sami kaiwa ga samun Ruwan Bagaja. Wannan a adabin baka kenan, da aka baddala wannan labari zuwa Ƙagagge, wanda ya samar da littafin Ruwan Bagaja, an sami sauyi na yanayi, inda maimakon a ambaci nau`o`in abinci da akan ci karo da su yayin biɗar, sai kawai a littafin aka musanya da haɗarurruka da aka rinƙa fuskanta wajen biɗar Ruwan Bagaja. Wannan shi ke nuna mana cewa an sami ragi a ainihin yadda adabin bakan yake. Wannan misali ne da ya shafi adabin baka da rubutacce, za kuma a iya samun irin wannan ragi na yanayi a adabin baka zalla wajen wanzar da su. Ba don komai ba sai don kasancewar mutane sun bambanta, kuma tun da adabin ba a rubuce yake ba, to ko shakka babu za a iya samun ragi wajen wanzar da shi daga wani wuri zuwa wani wurin.

### 4.3.3 Ragi na Ma’ana

Idan kuwa an sami sauyin isar da saƙo ko manufar adabin baka, an sami sauyi na ma`ana. Wato wanda ya ƙirƙiri adabin baka na da manufa ta musamman da suke son isar wa ga masu sauraro, matuƙar an sauya wannan manufa, musamman ta sauya wasu kalmomi da za su canza ma`ana ta asali, an sami sauyi na ma`ana. Yana da kyau a fahinci cewa akwai manufar ƙirƙirar kowane nau`in adabin baka. Yayin wanzar da su waɗannan nau`o`in adabin akan sami sauyi na manufar da ake son cimmawa. Wannan na faruwa ne ga masu wanzar da adabin bakan. Mai tattara adabin baka na iya fuskantar wannan matsala ta ragin manufa. Saboda yakan tunkari mutane da yawa wajen tattara nau`in adabin bakan da yake son tattarawa. Mutanen da yake tuntuɓa wajen tattara adabin, na iya sauya manufa ko saƙon da ake son cimmawa. Wannan na faruwa ta hanyar sauya wasu kalmomi ko tsarin da aka san adabin da shi. Ko ma dai mene ne, shekaru da fahimtar al`amari na iya shafar wanzar da adabin baka daga wannan al`umma zuwa ga waccan al`umma mai tasowa.

### 4.3.4 Ma’anar Ƙari

Ƙamusun Bayero, (2006:277) ya bayyana ma`anar ƙari a matsayin daɗin wanin akan wani abu. Wato daɗa wani komin ƙanƙanatarsa a bisa siffa ko yanayi na asali da ak san abu na das hi, wannan shi ake nufi da ƙari, wato duk wani abu da ya kasance an sami daɗi akan yadda yake tun asali, an sami ƙari kenan. Idan aka danganta da matsalolin tattara adabin baka, ana nufin cewa akwai inda ake samun ƙari ga siffar adabin baka walau ta yanayi ko ta siffa ko manufa, kamar yadda za mu gani a darasin nan.

### 4.3.5 Ƙari na Yanayi

A baya, an bayyana yadda ragin yanayi yake, waton rage wane abu daga asalin yadda yadda yake. Shi kuwa ƙarin yanayi ɗaya ɓangare ne na ragi. Ƙarin yanayi na nufi duk wani daɗi da aka samu na yanayin da abu yake tun asali. Ƙari ma na ɗaya daga cikin matsalolin da ke tattare da tattara adabin baka da adana shi. Sau da yawa akan sami sauye-sauyen na yadda adabin baka yake, misali akan sami sauyi a wasu labaran baka na wasa ƙwaƙwalwa daga wuri zuwa wani wurin. Haka nan kuma akan sami ƙari wajen wanzar da waƙa ko da kuwa waƙar daga bakin wanda ya yi ta tun farko ne. Idan ya zo wanzar da ita za a iya samun ƙari bisa yadda aka ƙirƙire ta tun farko. Haka na wanzuwa kasancewar abubuwan adabin baka ana ƙirƙirarsu a ‘ka’ a kuma adana su a ‘ka’, yayin wanzarwa a yi amfani da baki. Saboda kasancewar ɗan Adam ajizi ne, ana samun ƙari a wasu sassa na wanzar da adabin.

### 4.3.6 Ƙari na Ma'ana

In har ana samun ragi na ma`ana, to ko shakka babu za aiya samun ƙari na ma`ana. Ƙari a nan na nufin daɗin wani abu ga yadda aka san shit un farko. Da yake mutane suke wanzar da adabin baka, kuma halayya da ɗabi`u da yanayin gudanar da rayuwa sun bambanta, daga wuri zuwa wani wurin, samun ƙari wajen wanzar da adabin baka abu ne mai sauƙi. Dalili kuwa, tana iya kasancewa wanda aka samo adabin daga bakinsa ya kasance yana da bambancin tunani da yadda ya ɗauki rayuwa, misali idan kai mai tattara adabin baka ka ci karo da irin waɗannan mutane, nan da nan za ka iya gane an yi ragi ko ƙari ta hanyar tuntuɓar wasu daga cikin al`ummar wannan wuri. Idan kuwa wanda aka tuntuɓa shi kaɗai ya rage wanda ya san wannan adabin ko kuma shi kaɗai ya san wannan waƙar ko zantukan hikimar, za a iya samun ƙari ko ragi na ma`ana domin kuwa duk abubuwan da ya faɗa dole a ɗauke su a matsayin haka suke domin babu wani da za a tuntuɓa wanda ya san yadda abin yake.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

1. A bayyana abin da aka fahimta da ma'anar ragi da ire-irensa.
2. Ɗaya daga cikin matsalolin tattara adabin baka shi ne Ƙari, ko an yarda?

### 4.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi, an tattauna kan yadda ragi da ƙari ke shafar tattara da kuma adana adabin baka. An fahimci cewa ragi ma na iya kasancewa ta fuska biyu, wato ragi na yanayi da kuma ragi na ma`ana. Haka abin yake ga ƙari shima ƙari ya kasu kashi biyu : Ƙari na ma`ana da kuma na yanayi. Dukkan waɗannan suna zama tarnaƙi ga samo adabin baka da kuma adana shi.

### 4.5 Manazarta Da Waɗansu A bubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

Bergery, G. P. (1993). *A Hausa –English Dictionary and English Hausa Ɓocabulary*: Zaria. Ahmadu Bello Uniɓersity Press.

CNHN, (2006): *Ƙamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

## 4.6 Amsoshin Tambayo

**1** Ƙari.na nufi ƙara wani abu a cikin wani abu da aka adana. Kamar ƙarin ma'ana da ake yi a cikin rubutun adabi adananne. Haka zalika batun ragi shi ne rage wani abu a jikin wani abin na daban. Kamar dai a ce a rage ma'anar wani abu a cikin adabin wanda aka riga aka adana shi.

2 tabbas ƙari yana tattare da matsaloli a cikin adabi baka. Domin za a yi abin da ba dai-dai ba a zauna a kansa a yarda da shi. Da yake adabin baka ba rubutacce ba ne, ƙarin da aka samu, zai yi wahala a bambance ƙarya da gaskiya.

## Rukuni Na 4 Hikimomin Zantukan Baka Na Hausa

Kashi Na 1 Karin Magana
Kashi Na 2 Salon Magana
Kashi Na 3 Take Da Kirari
Kashi Na 4 Zaurance

## Kashi Na 1 Karin Magana

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma'anar Karin Magana ta Zahiri.
  1.3.1 Ma'anar Karin Magana ta Ɓoye
  1.3.2 Ire-Iren Karin Magana
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Auna Fahimta

### 1.1 Gabatarwa (Introduction)

Karin magana ɗaya ce daga cikin hikimomin sarrafa harshe da Bahaushe ke amfani shi wajen koyar da darussan rayuwa da kaifafa tunani da cusa kyawawan ɗabi'u cikin al'umma.
Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan karin magana da ire-irensa da kuma ƙunshiyarsa.

### 1.2 Manufar Darasi

Manufar wannan darasi ita ce koyar da karin maganar Hausa da ire-irensu. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma'anar karin magana
- Ire-iren karin magana na Hausa
- Bayyana matsayin karin magana a adabin Hausa

## 1.3 Ma’anar Karin Magana ta Zahiri

Kirk-Greene (1966) ya bayyana cewa karin magana na inganta al’adun al’umma da suka gada, da tarihin al’umma, da hikimomin al’umma. Bayan haka, a inda ba a sami rubutaccen adabi ba, karin magana na iya zama kafar tattara falsafar ƙasa.
Haka nan Zarruƙ da Alhassan (1982:3) sun bayar da ma’anar karin magana da cewa nazari ne na rayuwa a dunƙule cikin gajerun maganganu da misalai irin na hikima. Karin magana ba ta faye zuga ko kuɗa ba, sai dai gwanintar kwatance. Misali, “Komai nisan jifa, ƙasa za ta dawo”.

Shi kuwa Umar (1984) ya ce, “Karin magana wata magana ce ‘yar ƙil da ta ƙunshi zunzurutun ma’ana lokacin da aka yi bayani.

Birniwa (2005:57) ya ƙara bayyana ma’anar karin magana da cewa: “Gajeruwar jimla ce da ake sakaya ma’ana da ita, wadda idan aka warware ta za ta bayar da ma’ana mai tsawo, wadda mafi yawa kalmomin da ke cikinta ba su ƙunsa ba, sai dai suna da dangantaka da ita”.

Bunza kuwa, ya kalli karin magana ne a matsayin ɗaya daga cikin daɗaɗɗun abubuwa na adana a’adun kowace al’umma a duniya (Bunza 2006:283).

### 1.3.1 Ma’anar Karin Magana ta Ɓoye

Karin magana zance ne a dunƙule mai faffaɗar ma’ana, wato wata gajeriyar magana ce ƙunshe da ɓoyayyiyar ma’ana ko dogon bayani in aka warware. Shi ya sa karin magana take da siffofin da suka keɓenta gare ta, wato gajarta da gaɓoɓi biyu da dunƙulewa da kuma reɗe ko fid da wasu kalmomi da ba dole sai an yi amfani da su ba.

Da yake kalmomi biyu ne suka gina karin magana, wato ‘*kari*’ da kuma ‘*magana*’. Kari na nufin wani ɓangare ko rabi ko karyayye ko kuma rababbe. Magana kuma na nufin zance ko furuci ko kalami da mutum kan yi domin a fahimci abin da ke cikin zuciyarsa. Ke nan karin magana zance ne da aka yi wa giɓi ko aka karya shi ko raba shi ko kuma aka kawo wani ɓangare aka yi watsi da wani ɓangaren (Malumfashi, 2018)

### 1.3.2 Ire-Iren Karin Magana

Yawancin karin maganar Hausa ɓangare biyu gare su, ɓanagare na biyu shi ke ciko bayanin ɓangare na farkon. Misali:

i. "Allah na mutane", jaɓa ta ga bakin mijinta
ii. "Da haka muka fara", kuturu ya ga mai ƙyasfi.
iii. "Da sauran tsalle", in ji ɓarawon dankali.
iv. "Abin da daɗi", an ba mayya tsaron gawa.
v. "Yaushe kuma?", an ce da kuturu ka gama lafiya. Da sauransu.

**1.3.2.1 Karin Magana ta kai tsaye**

Karin Magana ta kai tsaye na nufin duk karin magana wadda take haka nan ba wani labari a cikin ta ita ake nufi da ta kai tsaye. Wata tana buƙatar ciko, wata kuma bat a buƙatar cikamako. Muhimmim abu ana nan shi, wata Karin maganar bayaninta a bayyane yake, wata kuwa sai an fayyace yadda bayaninta yake. Misalin:

- Gyarar fuska ta fi gyarar gona,
- Kyawawan kalamai sukan mayar da zaki tunkiya
- Durƙusawa Wada ba gajiya ba ce.
- Abokin ɓarawo, ɓarawo ne.
- Aiki ya yi wa kurege yawa, ya yi gina ya yi yasa.
- An kashe tsuntsu biyu da dutse guda.
- In kai min kan kara, zan yi ma na itace.
- In dai amarya ba ta hau doki ba, to ba ta ɗaukar kaya.
- Tuwon girma miyarsa nama.
- Ba ni na kar zomon ba, rataya aka bani.
- Yaba kyauta tukuici.
- Dajin wani, karkarar wani.
- Zama da maɗaukin kanwa, shi ke kawo farin kai.

**1.3.3.2 Karin Magana Mai Labari**

Irin wannan karin maganar takan zo ne ƙunshe da labarin wata aukuwa wadda ita ce ta haifar da samuwar karin maganar. Misali :

- Gaba ta kai ni, gobarar Titi a Jos.
- Shanunka sun bi shanun Sarki
- Ƙunar baƙin wake
- Gamo da katar.

A misali na farko, wata mata ce mai suna Titi a garin Jos ta yi gobara komai nata ya ƙone sakamakon gobarar ta yi asara mai yawa, ta shiga yanayi na damuwa. Amma sai jama'a suka yi ta kawo mata gudummawa, har ta tara dukiya da kayyaki masu yawan gaske fiye da na da kafin ta yi gobarar. Sai ta ce wannan gobara ai gaba ta kai ni. Tun daga nan aka sami karin maganar gaba ta kai ni gobarar Titi a Jos.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana ma'anar karin magana
2. Kawo ire-iren karin magana na Hausa

## 1.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi an tattauna a kan karin magana, wato dunƙulalliyar magana mai faffaɗar ma'ana wadda Bahaushe ke amfani da ita wajen koyar da darussan rayuwa da kaifafa tunani da cusa kyawawan ɗabi'u cikin al'umma. Kashin ya ƙunshi bayanai kan ma'ana da ire-iren karin magana na Hausa.

## 1.5 Manazarta Da Wasu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

Birniwa, H.A. (2005). Tsintar Dame a Kala : Matsayin Karin Magana a Cikin

Waƙoƙin Siyasa. In Ɗunɗaye Journal of Hausa Studies. Department of Nigerian Languages. Sokoto : Usman Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Bunza, A.M (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos : Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Serɓices.

Kirk-Greene, A.H.M (1996). Hausa Ba Dabo Ba Ne. Ibadan : Oɗford Uniɓersity Press.

## 1.6 Amsoshin Tambayoyi

**1** Karin Magana gajeren zance ko bayani marar tsayi mai ɗauke da ma’ana da azamci. Sai dai ba a fito wa a yi Magana kai tsaye. Karin Magana tana nuna ko bayyana ƙwarewar mai Magana da harshe

2 ire-iren Karin Magana

a. Karin Magana mai mahaɗi. Miisali mu gani a ƙasa inji kare ance ana biki a gidansu

b. Karin Magana mai Faɗakarwa: bin na gaba bin Allah

**c.** Karin Mgana Mai Gargaɗi. Misali: da muguwar rawa, gwamma ƙin ashi

## Kashi Na 2 Salon Magana

### Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ma’anar Salo
    2.3.1 Ma’anar Salon Magana
        2.3.1.1Ire-Iren Salon Magana
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Auna Fahimta

### 2.1 Gabatarwa (Introduction)

Salon magana ko ƙarangiya ko gagara-gwari ɗaya ce daga cikin hikimomin sarrafa harshe da Bahaushe ke amfani da su a zantukansa na yau da kullum domin ƙawata zance da ƙara armashin magana.

Wannan kashi ya ƙunshi bayanai kan salon magana da ire-irensa a Hausa.

### 2.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce koyar da salon magana a adabin Hausa da ire-iren salon maganar. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma’anar salo
- Ma’anar salon magana
- Ire-iren salon magana

### 2.3 Ma’anar Salo

Ɗangambo (1981:2-3), ya bayyana ma’anar salo a matsayin hanyoyi ko dabarun isar da saƙo. Wato salo ya ƙunshi zaɓi kuma kyan salo ko muninsa ya danganta da yadda mutum ya zaɓi abubuwan da ya yi amafani da su cikin rubutunsa ko furucinsa don isar da saƙonsa. Salo ya ta’allaƙa ne dangane da yadda mutum yake tunani cikin dacewa.

### 2.3.1 Ma’anar Salon Magana

Salon magana ko ƙarangiya ko gagara-gwari zance ne mai ɗauke ko ƙunshe da wasu kalmomi masu wuya ko masu kama da juna, yakan ƙunshi luguden kalmomi. Kenan, salon magana maganganu ne na hikima da kakkarya harshe waɗanda ake yi ta hanyar sarƙa kalmomi masu sauti iri ɗaya a cikin jimla ko jimloli, a yi magana mai sarƙaƙiya.

#### 2.3.1.1 Ire-Iren Salon Magana

Akwai ire-iren salon magana da dama a harshen Hausa, gwargwadon naƙaltar harshen mai magana. Mislai:

- Ina tafiya ta Kurun na tsinci kunkurun Kurun na kai ta kasuwar Kurun ana kurun ina kurun na sai da kunkurun Kurun.
- Turmi ture kura, kura ture turmi.
- Cab caɓe ƙashi, tsoka, tsotse, soke a faƙo.
- Haka silif na saluɓe siliya a wuyan Salamatu ashe ban sani ba an yi wa Salihu satar sintali a Salanta.
- Battar da ba ta da taba ba ta tabbata batta ba da tana da taba da ta tabbata batta.
- An kashe kasa, an kasa gwaza, garin kallon kasasshiyar kasa na kasa kwashe kashin gwaza.
- Tun da Taɓo take ba ta taɓa taɓa taɓo ba, sai da taɓo ya faɗo cikin taɓo sannan Taɓo ta taɓa taɓa taɓo.

**Auna Fahimta**

1. Bayyana ma’anar salon magana
2. Kawo ire-iren salon magana da aka sani

### 2.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi an tattauna a kan salon magana, da ire-irensa a matsayin dabarun ƙawata zance na yau da kullum. Kashin ya ƙunshi bayanai kan ma’ana da ire-iren salon magana tare da misalai.

## 2.6 Manazarta Da Wasu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Serɓices.

## 2.6 Amsoshin Tambayoyi

1. Bayyana ma'anar salon magana

   Salon magana ko ƙarangiya ko gagara-gwari zance ne mai ɗauke ko ƙunshe da wasu kalmomi masu wuya ko masu kama da juna, yakan ƙunshi luguden kalmomi. Kenan, salon magana maganganu ne na hikima da kakkarya harshe waɗanda ake yi ta hanyar sarƙa kalmomi masu sauti iri ɗaya a cikin jimla ko jimloli, a yi magana mai sarƙaƙiya.

   i. Ina tafiya ta Kurun na tsinci kunkurun Kurun na kai ta kasuwar Kurun ana kurun
   ina kurun na sai da kunkurun Kurun.
   ii. Turmi ture kura, kura ture turmi.
   iii. Cab caɓe ƙashi, tsoka, tsotse, soke a faƙo.
   iv. Haka silif na saluɓe siliya a wuyan Salamatu ashe ban sani ba an yi wa Salihu satar sintali a Salanta.
   v. Battar da ba ta da taba ba ta tabbata batta ba da tana da taba da ta tabbata batta.
   vi. An kashe kasa, an kasa gwaza, garin kallon kasasshiyar kasa na kasa kwashe kashin gwaza.

## Kashi Na 3 Take Da Kirari

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Ma’anar Take
3.4 Ma’anar Kirari
3.5 Bambancin Take da Kirari
3.6 Taƙaitawa
3.7 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
3.8 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.9 Amsoshin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa (Introduction)

Take da kirari tamkar abokan juna ne domin a mafi yawancin lokuta tare suke tafiya ko kuma take ya yi wa kirari sharar fage. Wannan kashi ya ƙunshi bayani kan ma’anar take da kirari da kuma bambance-bambancen da ke tsakaninsu.

### 3.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce koyar da take da kirari a adabin Hausa da ire-irensu da kuma bambancin take da kirari. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma’anar Take
- Ma’anar Kirari
- Bambancin Take Da Kirari

### 3.3 Ma’anar Take

Take ya samu ne daga kalmar *takawa*, wato a yaba ka ko kwarzanta ko zuga ka, da zai sa ka jirga ko ka taka saboda ka ji daɗin abin nan da ka ji ko saurara. Akan yi take da kiɗa ko wasu furuci da suke danganta abin da ake kaɗa wa taken da shi.

### 3.3.1 Ma'anar Kirari

Kirari furuci ne wanda ya yi kama da yabo, ta amfani da kalmomin cicciɓawa da ake yi wa wani mutum cikin hikima don a kambama shi ko wani abu don a fito da kyawonsa da armashinsa a idon jama'a.
Mutum na iya yi wa kansa kirari, ko ya yi wa wani ko wani ya yi masa. Alal misali :

i. Sai ni baƙi fentin Allah, mahaukacin kare mijin Ladidi
ii. Damo sarkin haƙuri ƙanin su Talatu
iii. Kunu ɗan babban masaki,

Shanka banza barin ka banza,

Da safe marmari da maraice ciwo,
Ya ɓata ruwa ya ɓata wuta ya je ciki bai yi komai ba,
A kira ka da tsinin baki a sha ka da tsinin baki.

### 3.3.2 Bambancin Take da Kirari

Bambancin take da kirari a bayyane yake. Take wani amo ko zance da ke share fage kafin kirari ya iso. Ana yin take ne da kiɗa ko busa ko wani salo da za a iya fassarawa a maganance. Misali, kafin fara farauta akan yi kiɗa don sanar da jama'a cewa za a fita, kuma wannan kiɗan yakan zo a matsayin taken wani ɗan farauta ne. Sa'annan take kan iya zama wani ɓangare na ƙoƙarin yabo ko kushewa ga abubuwan da jama'a suka sa gaba, sai dai take bai cika tsawo ba. Sai dai duk da yake take yana zuwa da amo ne, ba zance ko furuci ne ba, da zarar aka yi wa mutum take zai iya ɓugewa da yin kirari.

A tsarin kirari, za a kira mutum ne ta hanyar amfani da sunansa ko ta ambaton siffofinsa waɗanda abin tutiya ne ko a wajen mai yin kirarin. Har ila yau, kirari kan iya ƙunsar kalaman da in ba a muhalli na kirarin ba, ba sa ambatuwa kai-tsaye ga mutum. Misali kalmomi irin su 'shege' ko 'mahaukaci' ko 'arne' da sauransu.

Daga bayanan da suka gabata, mun fahimci ana gina kirari da siffa ko halayyar mutum ko abin da za a kirara, akan kuma danganta abu da makusantarsa misali miji da mata ko 'yan'uwa da sauransu. Sa'annan, ana iya yi wa mutum ko dabba ko gari ko abinci ko itaciya ko wani abu mai rai ko mara rai kirari. Shi kuwa take amo ne ake kaɗawa domin tsuma mutum (galibi) a fagen nuna bajinta kamar farauta ko yaƙi da sauransu). Sai dai kirari kan biyo bayan take ya yi masa ladanci.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

1. Bayyana ma'anar take da kirari
2. Ya ya tsarin kirari yake?

## 3.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi an tattauna a kan take da kirari. Kashin ya ƙunshi bayanai kan ma'ana da bambancin take da kirari tare da misalai.

## 3.5 Manazarta Da Wasu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)

Ɗangambo, A. (2008). *Rabe-Raben Adabin Hausa*. Sabon Tsari. Zaria : Amana Publishers

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Serɓices.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyi

1. Take ya samu ne daga kalmar *takawa*, wato a yaba ka ko kwarzanta ko zuga ka, da zai sa ka jirga ko ka taka saboda ka ji daɗin abin nan da ka ji ko saurara. Akan yi take da kiɗa ko wasu furuci da suke danganta abin da ake kaɗa wa taken da shi.

- Kirari furuci ne wanda ya yi kama da yabo, ta amfani da kalmomin cicciɓawa da ake yi wa wani mutum cikin hikima don a kambama shi ko wani abu don a fito da kyawonsa da armashinsa a idon jama'a.

2. A tsarin kirari, za a kira mutum ne ta hanyar amfani da sunansa ko ta ambaton siffofinsa waɗanda abin tutiya ne ko a wajen mai yin kirarin. Har ila yau, kirari kan iya ƙunsar kalaman da in ba a muhalli na kirarin ba, ba sa ambatuwa kai

# Kashi Na 4 Zaurance

**Abubuwan da Suke Ciki**


4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Ma’anar Zaurance
  4.3.1 Ire-iren Zaurance
  4.3.2 Yadda ake aiwatar da zaurance
4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma’anar Wasu Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.7 Amsoshin Auna Fahimta


## 4.1 Gabatarwa (Introduction)

Zaurance wani salo ne na ƙwarewar harshe da Hausawa ke amfani da shi a matsayin sadarwa ta sirri a tsakanin su. Wannan kashi ya ƙunshi bayani kan ma’ana da iren zaurance da kuma yadda ake aiwatar da zaurance a Hausa.

## 4.2 Manufar Darasi (Objectiɓes)

Manufar wannan darasi ita ce koyar da zaurance a Hausa da ire-irensa da kuma yadda ake aiwatar da shi. A ƙarshen wannan darasin, ana sa rai ɗalibai za su fahimci :

- Ma’anar zaurance
- Ire-iren zaurance
- Yadda ake aiwatar da zaurance

## 4.3 Ma’anar Zaurance

Zaurance salon magana ne da akan yi don a ɓad-da bami, domin kada ya gane inda aka dosa. Zaurance kan kasance tamkar wani yare ne na ɗan taƙaitaccen lokaci da ake ƙirƙira a cikin rukunin al’umma, saboda a nuna gwanancewa a harshe.

‘Yan mata ne suka fi yin zaurance, musamman a lokacin da suke son yin wata magana ta sirri wadda ba su son kowa ya fahimta, sai su kaɗai.

Sukan tsaya su tsara salon da za su riƙa yin maganar da ba mai iya gane ta sai su kaɗai.

Masana irin su Ɗangambo, (2008) sun bayyana Zaurance da cewa: shi ma sarrafa harshe ne, da ke cike da hikima. Zaurance, ƙirƙirarren harshe ne. Akan ƙara wa kalmomi ko kuma gaɓoɓin kalmomi wasu kalmomin ko gaɓoɓin, a mai da su sababbi, yadda idan mutum bai naƙalci yadda abin yake ba, to, ba zai gane abin da ake nufi ba. Ana iya ƙara duk abin da aka ga dama, don a yi wannan ɓad-da-bami. Misali, za a iya ƙara wa gaɓoɓin kalmomi sautukan b, c, d, f, g, h, j, k, da dai sauransu. Ga wani misalin zaurance wanda ake ƙara *da:*

| | | |
|---|---|---|
| Musa | = Mu-du-sa-da | = Mudusada |
| Mairo | = Ma-dai-ro-do | = Madairodo |

Ka-dai ma-dai ka-da-ra-da-tu-du = kai mai karatu
Za-dan-ce-de, ko-do ba-da ka-da = zan ce ko ba ka gane ba? ga-da-ne-de- ba-da?

Na-da-je-de-ka-da-su-du-wa-da = Na je kasuwa.

**Ma'ana:** Kai mai karatu, ka gane wannan zance, ko ba ka gane ba? A nan, za a lura cewa, ana ƙara wa gaɓoɓin kalmomi da ne, sai dai ƙarin, yana shafar wasulla ma; idan ma akwai ɗauri, baƙi (harafi), shi ma abin yana shafar sa. Misali:
Idan gaɓar tana da wasalin *a,* to *d* ɗin da aka ƙara, shi ma sai a sa masa *a,* idan *e* ne, sai a sa wa *d* ɗin e, da dai sauransu. Idan kuwa ɗauri ne, misali, *kai, sai, mai, tau, ƙin* da sauransu, to, nan ma, akan yi wa haruffan ɗaurin bayan *d* ɗin. Misali, *ka-dai, sa- dai, ma-dai, ta-dau, ƙi-din,* da sauransu.

### 4.3.1 Ire-iren Zaurance

Abin da ke sama misali ne na zaurance guda ɗaya. Za a iya samun zaurance iri daban daban, wannan ya danganta da irin ƙarin da aka yi kalma ko kuma gaɓoɓin muryoyin kalmonmi.

### 4.3.2 Yadda ake aiwatar da zaurance

Ana yin zaurance ne ta hanyar ƙara wasu harrufa a ƙarshen kowace gaɓa da ke cikin kalma har zuwa ƙarshen zancen. Har ila yau, babu wata ƙa'ida da aka ajiye cewa lallai sai harafi kaza za a yi amfani da shi. Illa masu yin zaurancen ne sukan zaɓi salon da suka so. Shi ya sa ma waɗannan ba su gane na waɗancan.

Zaurance na koyar da muhimmancin riƙe sirri da neman shawarar juna da haɗin kai da amince wa juna da riƙon amana, da kuma son juna.

**Auna Fahimta (Tutor-marked Assignment)**

1. Bayyana ma'anar zaurance
2. Kawo ire-iren zaurance

## 4.4 Taƙaitawa (Summary)

A wannan kashi an tattauna a kan zaurance. Kashin ya ƙunshi bayanai kan ma'ana da ire-iren zaurance da kuma yadda ake aiwatar da zaurance.

## 4.5 Manazarta Da Wasu Abubuwa Na Ƙara Nazari (Referenc/Further Reading)


Abrams, M.H. (1981): *A Glossary of Literary Terms.* Siɗ Edition Halt Rinehart & Wiston, New York.

Abdullahi, B.Y. (2001): *Salo Asirin Waka* Fisbas Media Kaduna.

Ahmed, U.B (1985) *Nau'o'in wasannin kwaikwayon Hausa*. Cibiyar Nazarin Al'adun Nijeriya. Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Ayindaho, K. (1985) "The Present State of African Literature Studies" In *African*

*Literature Studies: The Present State*. Ed Stephen Arnold, Washington; African Literature Association & Three Continent's Press.

Babajo, A. K. (2011). *Orature: Meaning, Nature and Forms*. A Study Guide for Undergraduate, Kaduna: Slimline Communication.

Bergery, G. P. (1993). *A Hausa –English Dictionary and English Hausa Ɓocabulary*: Zaria. Ahmadu Bello Uniɓersity Press.

Birniwa, H.A. (2005). Tsintar Dame a Kala : Matsayin Karin Magana a Cikin

Waƙoƙin Siyasa. In Ɗunɗaye Journal of Hausa Studies. Department of Nigerian Languages. Sokoto : Usman Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Bunza, A. M. (2002) "Nazarin Al'adun Da Ke Cikin Kaset-Kaset Na Hausa Da

Littafan Zamani (1980 – 2002)". Maƙalar Da Aka Gabatar A Taron Ƙarawa Juna Sani Jami'ar Usman Ɗanfodiyo Sakkwato.

………………. (2006) *Gadon Feɗe Al'ada.* Tiwal Nigeria Limited, 16th Akinbaruwa Street, Off Atunrase Street, Surulere, Lagos.

……………….. (2011) "Al'adun Hausawa Jiya da Yau: Ci Gaba ko Lalacewa?" Takardar da Aka Gabatar a Taron Bukukuwan Ɗalibai na Makon Hausa. Sashen Nazarin Harsuna Nijeriya da Ilimin Harshe, Jami'ar Jihar Kaduna, Kaduna.

Cuddons, J.A (1977). *A Dictionary of Literary Terms*. Reɓised Edition, London.

Ɗangambo, A. (1984): *Rabe-Raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa Ga*

*Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph Publishers.

Ɗangambo, A. (2007). *Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa*. Kaduna: Baraka Press and Publishers Limited.

Finnegan, R. (1970). *Oral Literature in Africa*. Odford: Odford Uniɓersity Press.

Garba, S. (2011). "Salon Sarrafa Harshe A Waƙoƙin Aƙilu Aliyu". Kundin Digiri na Uku. Zariya: Sashen Harsuna Da Al'adun Afirka, Jami'ar

Ahmadu Bello.Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Serɓices.

Gusau, S.M (1995). *Dabarun Nazarin Hausa*. Kaduna : Fisbas Media Serɓices.

………………(2003). *Jagoran Nazarin Wa}ar Baka.* Benchmark PublishersLimited, Kano.

………………(2006). Tatsuniya (Gatana) : Sigoginta da Hikimominta. Cikin *Mujallar Algaita*, 4,1.

………………(2008). *Waƙoƙin Baka A Ƙasar Hausa: Yanaye-Yanayensu Da Sigoginsu.* Kano: Benchmark Pulishers Limited.

………………(2009). Diwanin Waƙoƙin Baka: Zaɓaɓɓun Matanoni Na Waƙoƙin Baka Na Hausa. Kano: Century Research and Publishing Limited.

………………(2014) *Diwanin Waƙoƙin Baka.* Juzu'i Na Biyu: Century Research and Publishing Limited Kano-Nigeria.

Khalil, I. (2009) Cakuɗe cakuɗen al'adu a fina-finan Hausa. Kundin Digirin Na Biyu Jami'ar Usman Ɗanfodiyo Sakkwato.

Kirk-Greene, A.H.M (1996). Hausa Ba Dabo Ba Ne. Ibadan : Oɗford Uniɓersity Press.

Lado, R. (1964): *Language Teaching* – A Scientific Approach, McGraw-Hill: New York.

Lenneberg, E. H. (1967): *Biological Foundations of Language*, Wiley, New York.

Liman, A. A. (2008) "Hegemony and Mass Mediated Culture: A Study of Popular Culture Trends in Postcolonial Northern Nigeria" Ph.D Thesis. Department of English, Faculty of Arts, Ahmadu Bello Uniɓersity Zaria.

Lorentzon, L. (2007). Is African Oral Literature Literature? *Research in African Literatures, 38*(3), 1-12. Retrieɓed February 7, 2020, from www.jstor.org/stable/20109492

Malumfashi, I. (2019): "Kunnenka Nawa? Labarin Hausa a Rubuce" a Cikin *Labarin Hausa a Rubuce 1927-2018* ISSBN: 978:978-55352-8-0. Zariya: Ɗab'in Maɗaba'ar Jami'ar Ahmadu Bello

Muhammad, Ɗ. (1978). "Waƙa Bahaushiya". cikin *Studies in Hausa Language, Literature And Culture*. Kano: Bayero Uniɓersity.

Mujaheed, A. (2018). "Hankaka Mai Da Ɗan Wani Naka: Waƙoƙin Salisu Sa'in Makafin Zazzau a Bakin Mawaƙan Ƙarni na 21". *Kadaura: Journal of Hausa Multi-Disciplinary Studies,* Ɓol. 1, No. 4, Special Edition. Department of Nigerian Languages and Linguistics, Kaduna State Uniɓersity-Nigeria.

Mukhtar, I. (2004). *Jagoran Nazarin {agaggun Labarai.* Benchmark Publishers Limited, Kano.

……………..(2004). *Introduction To Stylistics Theories, Practice And Criticism*. Abuja; Country Side Publishers Ɓol. I.

Okoh, Nkem. (2008). *Preface to Oral Literature*, Africana First Publishers Limited, Books House Trust, Onitsha Nigeria.

Okpewho, I. (1990). *Oral Performance in Africa*. Ibadan Spectrum Books. Ltd.

…………. (1992). *African Oral Literature*. Bloomington IN Indiana Uniƃersity Press.

Rabi, M. (2011): "Ɗabi'un Mata a Bakin Mawaƙan Baka na Hausa" Kundin Digiri na Biyu, Sashen Harsuna da Al'adun Afrika, Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya (2013) *Makaɗi A Mahangar Manazarta:* Jerin Takardun da Aka Gabatar a Taron Ƙara wa Juna Sani Kan Tubar Muhammadu Gambo Mai Kalangu, Gidan Dabino Publishers.

Satatima, I.G.(2009). "Waƙoƙin Baka na Ɗarsashin Zuciya: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu." Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Shipley, J.T. (ed) (1955). *Dictionary of World Literary Terms.* Allens & Unwin Ltd London.

Taylor, E. (1871). *The Science of Culture*. Cambridge Uniƃersity Press.

Yakasai, S A. (2012). *Jagorar ilimin Walwalar Harshe*, Sokoto. Garkuwa Media Serƃice Ltd.

Yahaya, A. B. (1997). *Jigon Nazarin Wa}a* Fisbas Media Serƃice Kaduna.

Yahaya, I.Y. (da wasu) (1992). *Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare* 1 – 3, Ibadan Uniƃersity Press.

## 4.7 Amsoshin Tambabyoyin Auna Fahimta

1. Zaurance salon magana ne da akan yi don a ɓad-da bami, domin kada ya gane inda aka dosa. Zaurance kan kasance tamkar wani yare ne na ɗan taƙaitaccen lokaci da ake ƙirƙira a cikin rukunin al'umma, saboda a nuna gwanancewa a harshe.
2. Ka-dai ma-dai ka-da-ra-da-tu-du = kai mai karatu
   Za-dan-ce-de, ko-do ba-da ka-da = zan ce ko ba ka gane ba? ga-da-ne-de- ba-da?
   Na-da-je-de-ka-da-su-du-wa-da = Na je kasuwa.